*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 13_14

___durk'usawa yayi a gabanta yace please beautiful ki saurareni wlh tunda naganki naji nasami matar aure ko banyi miki bane Ladidi ce ta yamutsa fuska kana tace bancema haka ba"mik'ewa yayi yace sunanan Amar jitayi sunan yayi mata d'adi sosai Ladidi ce ta fad'amai asalin sunanta wato khadija wow Amar yace daganan yace kozan iya d'aukar ki a mota ,ta eh tace babu damuwa daganan ya maidata gida sunyi musayar number tashige gida mom ce take tambayarta daga ina take cewa tayi daga gidansu yar ajinmu ne naje dubota babu Ipy momy ce ,tace to kiyi sallah kici abinci semu shiga kitchen ".

Bayan tayi sallah taci abinci ta d'auko wayarta tana duba massage number Amar tagani ya rubuto mata sak'on" kin budewa tayi saboda batason seta fara karantawa momy ta kirata kuma taga sak'on da yawa tana shirin tashi tajiyo kiran momy amsawa tayi ta jona wayar tata a charge ta,tafi kiran direct kitchen tawuce tasami momy tana had'a kayan buk'ata na girki saboda yanzu tare sukeyin girki ummi tayi aure kuma bata nemi yar, aiki ba".

Bayan sun gama girkin ta nufi d'akinta ta gyara dan sam batason k'azanta shiyasa komai nata tsaf ,tsaf bayan sallahr isha,I tana shirin karanta massage d'in Ammar sega kiranshi nan yashigo muryarshi me sanyi ce tadaki dodon kunnenta kirari yafara yimata yana wasata godiya tayi mai daganan suka gaisa "rungume fillow yayi ,yace kinsan me khadija ¿a,a tace yaci gaba

dacewa wlh jinakeyi ,inama kena rungume ba fillow ba murmushi tayi kana tace to mekakeci naba na zuba ".

Dambu yace suka suka sa dariya" tambayarta yayi kinayin whtsapp ne ¿"a,a tace mai Amar ne yace to meyasa¿Ladidi ce ,tace ra,ayina ne hakan shiru yayi kana yace inason zuwa hira yaushe kikeso inzo shiru tayi nad'an wani lokaci kana tace zanyi shawara"Amar ,ranshi ya 6aci amma be nuna mata ba sukayi sallama "bacci ya gagara d'aukar shi se tunanin Khadija yakeyi wato Ladidi yarasa wane irin so yake yimata sona sha,awa ne kokuma so na zuciya se juyi yakeyi "jiyayi mararshi tashiga ciwo yarasa ina zesa kansa yaji dad'i wata babyn shi yakirawo da sukeyin masha,arsu ".

*WAYE  AMAR*
Amar d'a ne ga Alhaji atiku dollars yataso cikin gata da kulawa sam bashida tarbiyar kuma baya tare da iyayenshi a London suke da zama tun mahaifan Alhaji Atiku suna London har aka haifi Alhaji Atiku shikad"ai Allah yabasu shiyasa basa,son lefin Alhajin shiyasa gatan da iyayen Alhaji Atiku suka bashi,shi yabawa d'anshi a ganinshi ,shine birgewa" Amar yaza6i yayi karatu a Nigeria shiyasa yabar iyayenshi yazo Nigeria yana karatu bashida kowa a Nigeria shiyasa yake abinda yaga dama y'an matanshi sunfi a k'irga "yanzu gashi Allah ya had'ashi da Ladidi kuma indai yaso abu to seya mallakeshi yake samun nutsuwa" gashi Allah yad'ora mai yawan sha,awa baya sati beyi sex da mata ba' gashi kya kyawa "wanan kenan.

Washe gari bayan Amar yaji sauk'i yakira Ladidi  a waya ringin d'aya ta d'aga wayar jin muryarshi tayi wata " iri"cewa tayi Ipy Amar najika haka¿Ipy yace mata ya nisa,yace beauty kin hanani barci"zaro ido Ladidi tayi 'kamar yana ganinta".

Tace nikuma "eh yace kinsani wanka zeci gaba tace momy na kira na bari,inje in dawo katse wayar tayi'ta dafe k'irjinta tunda take Allah beta,6a had'ata da mara kunyar saurayi kamar Amar ba".

Yau kwanansu hud'u da had'uwa ,yaune Amar yakira Ladidi a waya ,yake gaya mata, bashi,da Ipy " hankalin,ta yayi mutuk'ar tashi tarasa yanda zatayi ta fad'awa momy saboda tanason zuwa gaishe,shi".ganin shiru,shiru "bata zoba yasa,shi neman number ta" wayar nata ringin amma tak'i d'agawa saboda yau Humaid na gida shikuma Jalal yatafi gurin sana,arsa.

Ranshi ya 6aci sosai"amma ya,d'au alwashin,shirin dayakeyi a kanta , momy ce ta,k'awala mata, kira amsawa tayi "da,sauri ta'amsa' bayan ta gyara  fuskar,ta " tana ganin kamar momy zata gano damuwa shimfid'e a fuskar ta,da sallama tashigo palon momy,samun guri tayi ta zauna"kana tace momy gani .

Momy ce ta dubeta ,tace khadija meyasa bakyason  fad'amin damuwar,ki "murmushin yak'e tayi kana tace momy wlh bani'da wata damuwa kawai tunanin karatu nakeyi" momy badan ta yarda'ba tace to shikenan kinci abinci kuwa eh tace suna cikin magana tajiyo wayar momy na ruri"tashi tayi taje ta'd'aukowa momy wayar,ta momy ce tace waye yake kira¿"Humaid ne Ladidi taba momy amsa to ki d'aga mana jiki na rawa ta d'aga wayar da sallama jin muryar mai maganar yasa'shi daka mata tsawa ,cewa yayi ubanwa yabaki ,ikon d'aga waya momy na "nakira ba keba rau'rau tayi da idanu momy taga yanayin'ta amma bata ce komai ba yak'ara da kicewa Ummi ta,kawomin abinci to 'tace ta ajiye wayar momy ce tadubi ladidi tace meya,ce miki ¿"Ladidi ce tace wai Ummi ta  kaimai abinci momy ce tayi murmushi kana tace to meyasa baki cemai Ummi takoma garin su Ladidi da idan ta yakawo k'awllah tace bakomai momy barin je in kaimai ,momy ce tayi'mata Allah ya shi albarka Ladidi tanajin dad'in wanan kalmar sosai shiyasa takeson momy bata'son 6acin ran'ta .

Kitchen ta wuce tazubo mai abincin ta had'o da juice me sanyi ta nufi hanyar da zata sadata da ,d'akinsu Humaid kasancewar da nisa a tsakanin'su da isar'ta " tayi nocking batayi magana ba" k'ara buga k'ofar tayi Humaid ne yace ubanwaye'yake damuna "shiru tayi bata'ce komai tura k'ofar tayi da sallama tashiga d'akin ganin halin da,yake ciki'ne ya sata sake kular abincin da kofin da'ta d'auko juice d'in zata gudu ya kamo ta ya k'ulle k'ofar.

Munafuka waya baki,izinin shigo'min d'aki " tayi mamakin sosai amma tasan ba acikin hayya'cinsa yaje ba "kwalbar giya ce 'a gaban shi se kwalin taba ya birki'ta d'akin " Ladidi ce takuma rugawa da ,gudu k'ofar d'akin tanufa"amma ina taji a kulle duban ta "takai ga Humaid da idanuwan shi sukayi ja kamar gauta tace please brother kabud'e,min k'ofa wlh nomy zata neme,ni shiru yayi yakuma duban 'ta mik'ewa yayi jiki na rawa yace baby kinzo a lokacin da nakeda buk'atar ki Ladidi ce ta mai'maita sunan da yakira ta wai baby tafiya yakeyi yana layi alamun yasha ya bugu ya matso kusada ita sunajin 'numfashin juna matsawa tadingayi shikuma yana binta kamar k'aramin yaro saida ya kaita bango tukun ya rungume'ta runtse idanun tayi wasu hawaye masu zafi na zubo mata jin alamun tudun breast d'inta yasa,shi rud'ewa " je'fata kan makeken gadon,shi yayi yafara had'e fuskar su guri d'aya"Ladidi kuka takeyi kamar,ranta ze fita tuno nasihar Yadikon,ta "tayi tashiga ture Humaid daga jikinta amma ko turuwa bayayi dake ingar'man ,namiji ne k'arfin ta ,ta had'a da cizo ta yak'ushi ta tureshi tana mikewa ta hango key, tabud'e k'ofar zata fice ya kamo'ta baya tayi da k'afarta ,ta tokare,shi ya fad'i a bakin k'ofar " ta fito da hawaye sha6e,sha6e a fuskar ta duk wanda yaganta yasan tana cikin damuwa Allah yatema keta tunda ta fito daga part d'in Humaid babu wanda ya ganta .

{K'ALU BALE GAREKU Y'AN MATA BA WAYON'KIBA BA DABARAR,KIBA ADU,A ITACE TAKI ALLAH YABAKU MIJI NAGARI DUK MACEN DA TABI DUNIYA TO TABBAS DANA SANI SHINE KARATUNTA ,KAR SOYAYYA TA RUFE MUKU IDO KUCE AI ZE AUREKI INA WLH BA AURANKI ZEYI BA .}..✍✍✍

Mom Islam ce ✍️✍️

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 15_16

______gado tafad'a taci gaba da rera kukanta a yanzu ko san taga Humaid batayi "misalin k'arfe shida na yamma tafito zuwa ,kitchen tasamu momy tagama komai sedai jera abinci a dining, temaka mata Ladidi tayi suka k'arasa.

"Washe gari ammar yakirata a waya, yake gaya mata tazo tarakashi gidan su k'anwar momyn'shi " cewa tayi zatazo amma seta tambayi momyn ta ,cikin farinciki ammar ya sa aka

,gyara gidanshi aka feshe gidan da turaruka masu tsada.

Washe gari Ladidi takira Ammar a waya tacemai yazo ,misalin k'arfe sha biyu na rana yazo ya d'auketa ,jin haka ya buga tsalle yana murna" suna cikin haka ne yake tambayar ta ,wane colorn abinci tafiso?dariya tayi kana tace indomie "cikin jin dad'i yace to karki damu drinks fa ?kowanne tace ,sukayi sallama .

Washe gari misalin k'arfe sha d'aya na rana Ladidi tagama komai tasami momy take gaya mata zataje gurin wankin kai " momy ce tace kije ki tambayo dadynki tunda yana gida.

Da sallama tashiga parlour n dady ,samunshi tayi yana waya bayan yagama ne ta gaishe'shi cikin ladabi ya amsa "sekuma ta sunkuyar da kanta k'asa dady ne yace Khadija meyafaru?cikin jin nauyi tace dama inason zuwa gurin kitso ne" dady ne yace to gashi su Humaid basanan ,amma kisa driver ya kaiki" to tacewa kana tamik'e zata fita.
Kiranta yayi ,yabata kud'i ,godiya tayimai ta fice ."

Zuwa tayi parlourn momy tagaya mata dady 'ya barta kuma yabata kud'in kitson"nasiha momy tayi mata daganan ta d'auko hijab d'inta ta fice, taje tayiwa driver magana tafad'a mai 'inda ze kaita "

Bayan sunje suna hanyar dawowa suka ,hango motoci bak'ak'e sun zagaye su ,babu  hanyar da zasu ,wuce "

Bude murfin motar tayi ,
baba  driver   ne yace"wallahi Khadija karki fita, Ladidi 'da hankalin ta ya tashi tace karka damu yanzu zan dawo ficewa tayi a motar, ta nufi gurin masu bak'ak'en motocin'nan bata hango kowaba acikin motar ,zata juya ta koma ,tasu motar "taji an janyota an turata mota,baba driver ne ya fito yana salati kafin yakai gurin masu motocin ,tuni suka wuce da gudu ,Baba megadi yara yazeyi ,mezeje ya fad'awa su Alhaji " driving yakeyi amma hankalin shi baya jikin shi ,haka ya iso gidan .
Momy ce dake shirin fita anguwa taji  Horn d'in baba driver ,bayan yafito daga motar ne ya durk'usa kana yagaida momy'mom daketa lek'en ta ina Ladidi zata fito "baba driver ne yace hajiya wlh tsau'tsayine yafaru da Khadijan " momy da bata,gane inda yadosa ba tace mekake nufi "koba tare kuka fita da khadija ba ¿" shiru yayi cankuma yace wlhi Allah hajiya muna cikin tafiya mukaga wasu a wata bak'ar mota ,yabata labarin inda akayi har cemata da yayi karta fita.

"Cikin tashin hankali momy ta ,kalli baba driver tace kuma ka iya dawowa saboda ragon azanci baka bisu ba ko"

"Kana ganin kai rayuwar ka tafi  ta kowa muhummanci .
Shiru drivern yayi kana yafara da ayi hak'uri hajiya ,momy cikin fushi tace ai wlh zakayi dana sani bari alhaji yadawo .
Waya sani ma koda sa hannunka a tafiyar da 'akayi da ita".

" cikin rud'ani driver yace ,wlhi hajiya babu sa hannun' na momy ce cikin fusata da 6acin rai tace shot up your mouth .

"Tace wlh idan kasake magana senayi report d'inka gurin police "zaro ido driver yayi kana yabar gurin ,momy da hankalin ta yagama tashi tarasa wace kalama zata ,fad'awa dady idan yadawo".

Shigewa part d'inta 'tayi ganin Humaid a ,zaune yasata ware ido tace" wato kai bakaji tashin' hankalin dake faruwa ba"Humaid da hankalin shi yatafi gurin TV a tsorace ya d'auki remote ya ,kashe kallon kana yamaida hankalinshi,gurin momy 'yace momy meke faruwa?"

Momy da idanuwan'ta suka ciko da hawaye ,tashare tadubi Humaid tace "tunda Khadija ta fita wlh ba,a gantaba a tsorace Humaid yace" bangane ba momy .
Momy na kuka tabashi labarin da 'driver yabata, a zabure Humaid ya mik'e ya'yi hanyar fita waje ,momy da keta kiranshi yak'i juyowa bare ya saurareta.

Kai tsaye gurin baba driver yanufa ,tunda baban ya hango shi ya fara salati,saboda dama basa shiri da Humaid ."

Cikin azama Humaid ya ,nufi gurinshi yana zuwa ya cakumo wuyar 'rigar baba driver yace gidan uban wa kakai marainiyar Allah "baba driver daya gama tsorata yace yaro " karka manta shekarata goma ina aiki a gidannan kuma ba,a ta6a samun matsala ba, seyanzu ne zance zan cutar da wani".
Humaid da bayajin ko mai da baba driver yake cewa yadinga ball dashi ,har seda momy tajiyo hayaniyar su tazo tana yiwa Humaid fad'a"

"Hak'uri tabawa drivern,ta ruk'o hannun Humaid suka shige ciki , tana cikin yimai fad'a sega Jalal nan ya k'araso ,ganin fuskar momy da Humaid babu fara'a yasashi k'arasowa da sauri yana momy meys faru " Humaid cikin k'unar zuciya yace Khadija cefa driver ya 6atar da ita "a zabure Jalal ya mik'e yace shine bro ka barshi? "Momy ce tadubi Jalal tabashi labarin da driver yabata Jalal yace wlh k'arya yakeyi" momy cikin d'aga murya tace zan sa6a muku "kubari dadynku yadawo ."

"Da daddare dady 'yashigo da fara,arsa ,rungumo momy ,yayi seyaga tak'i yin dariya alhalin ba haka tasaba yimai ba" duba fuskarta yayi kana yace hajiya meke faruwa naga kin sauya cikin tashin hankali da muryar da taci kuka ,tace Khadija .
Dady ne yace meyafaru da Khadijan¿ momy tace barin kirayo maka driver "mik'ewa tayi ,dady ganin momy tayi waje yasa'shi mik'ewa tare suka fita .

Tunda suka isa parking space d'in momy take ta k'awalawa driver kira ".

A hanzarce ya fito cikin ladabi ya gaida dady ' dady ne yace meyafaru ne da Khadija ?"
Cikin fad'uwar gaba driver yabawa dady labarin abinda yafaru dasu .
Kid'imewa dady 'yayi yahau fad'a ,yana cewa wlh baku kyauta minba meyasa ba'a kirani a wayaba "momy da kuka ya ku6uce mata ,takasa magana ,dady ne ya d'auki motarshi ya nufi police station yayi musu bayani ".

Tare dakawo photon Ladidin dakuma kalar kayan da tasa .

Bayan su momy sun dawo gida,suna zaune da safe ,suna kallo a TV sukaji ana cigiyr Ladidi momy jitayi hawaye sun zubo mata,dady kuwa hak'uri yake bata amma shima yanajin cikin zuciyarshi babu dad'i".

Tunda Ladidi ta 6ata momy tadena jin dad'in aiki sosai ,seda tasa aka d'auko mata yar aiki .

*WAYE YA SACE LADIDI*

Tunda suka sata a mota suka rufe mata fuska da bak'in wani abu, ihu takeyi 'iya k'arfinta amma babu wanda ya kulata, jitayi an d'auketa ana tafiya da ita ,daganan taji an sauketa an zaunar da ita an wurgo mata Jakarta .
Takai minti talatin a haka can kuma taji an bude mata ido,ganin ta a wani k'ayataccen parlor yasata sakin kuka tana, kiran momy " Ammar ne yafito d'auke da plate na abinci a wani farin trai me adon flowers masu kyau.
Ajiye mata yayi a gabanta ,nunashi tashiga yi da 'dasha shiyar muryar ta 'tace Ammar wanan ce soyayya ? ta k'ara dacewa wlh ka cuci kanka kuma tayarwa da iyayena hankali da kayi se Allah, yayimin sakayya .✍️✍️✍️

Mom Islam ce✍️✍️✍️

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 17_18

_____Dariya ma tabashi ,seda yayi mai 'isarshi kana yace "kin mance da masoyinki ko ?kin kulashi tayi,sekuma taji hawaye na zubo mata .
Ammar ne yaturo mata abincin kana yace kici abinci " dama kince kinfison indomie ,kuma ita na dafa miki .
Kici kiji girkin Ammar d'inki "cikin masifa tace tirr !da hali 'irin 'naka ,tuno halinta na da lokacin da take k'auye tayi ,shirin mugunta take yimai .

" Tace to yanzu ka maidani gida" wani 'irin kallo yayi mata, ina wanan brother naki mara mutunci "cikin fusata tace bangane ba ¿" dariya yayi mata irin 'na y'an duniya yace manta.
Jiyo k'arar wayarta tayi dake hand bag d'inta ,zata d'auka Ammar ya kwace wayar ,cikin masifa tace wlh koka bani wayata kokuma kayi nadama"yayi receive din kiran kenan , zeyi magana da alamu han,kalinshi na kan wayar yana shirya iskancin daze fad'a musu .
Ficewa yayi a parlor yana tunanin ai bazata fice ba".

Bud'e k'ofar tayi a hankali tayi waje babu hijab a jikinta babu takalmi, lek'awa tayi taga babu megadi ,ta bud'e k'ofar da gudu ta ruga tanata gudu ,tarasa inda zata nufa .
A wata anguwa mesuna rikos ta tsaya tana jiran mutane ,hango wani yaro tayi ze shiga wani gida."

Azama tayi ta isa gurin yaron kana tafara tambayar shi ,dan Allah yaro daga nan zuwa 6ukur park G.R.A dan Allah nawa ne ? yaron yace" masu napep zasu kaiki a d'ari biyu ,godiya tayi mai tacigaba da tafiya.
Tana cikin tafiya ne ta hango wani me adai,daita yace hajiya ina zuwa "anguwar ta fad'amai,

yace " tashiga su tafi ."

Sunyi tafiya me nisa sanan suka iso anguwar ,a lokacinne tafara gane anguwar tasu,nuni tayi mai da ga'gidan can "barinje in kar6o maka kud'inka ."

Me napep ne yashiga yimata masifa yana cewa dama kinsan bakida kud'i kika shiga to wlh inan a nan kishiga ki fito ".
Tana shiga taci karo da Jalal ,yana ganinta yahau tuhumarta" Ladidi cikin jin tsoron abinda ze biyo baya tace dan Allah brother dari biyu zaka bani 'inbawa me napep "Jalal ne yace gashi mik'a mai ".
Fita tayi tabashi ya tafi,tadawo cikin gidan.
Bata sami Jalal din waje ba ,tashige cikin gidan ,tana shiga tayi sallama ta hango momy da Humaid da Jalal da ,dady saboda baije aiki ba.
Tunda dady'ya hangota yafara yimata wani kallo tana shigowa ,Humaid ya mik'e ya wanka mata tagwayen maruka har biyu,babu wanda yayi 'yink'urin hanashi .
Cikin 6acin rai Humaid yace gidan ubanwa kikaje" banza mara tunani" Ladidi da tarasa mai zatace tadubi dady da tun shigowar'ta yake kallon ta 'taje har gabanshi tana kuka tace wlh dady ba wani guri naje ba "ya d'aga hannu zekai mata mari momy ta rik'e hannun tace katsaya muji abinda zatace" ai alamun mai gaskiya ya fita da ban .
Dady ne ya saurara,yana jiran mezatace cikin murya mai ban tausayi Ladidi tace wlh dady dama cemaka nayi zani gurin kitso ,to bayan an yimin muna cikin dawowa da driver mukaga wasu ,bak'ak'en motoci sun zagayemu "shine na fita inyi musu magana ,naji anturani cikin mota an rufemin fuskata ,an kawoni wani gida kuma bansan inda jakata take ba " momy ce tadubi Ladidi tace to d'azu da Jalal yakira a wayarki waye ya d'auka? cikin she' shek'ar kuka Ladidi tace lokacin da aka shigo dani cikin wani gidan shine naga babu kowa a gidan ,cankuma naji motsin,fitowar mutum.
Bayan mutumin ya fito shine , naji alamun ana kira a wayata ,ashe wayar na gefena "nazo d'auka naji an kwace wayar" da mutumin yashige ciki nikuma na gudo ".

Dady ne ya jinjina lamarin yace " amma kinsman shine ?atsorace tace wlh dady bansan shiba ,su Jalal da Hunaid 'da suka zuba mata ido suna kallon ta ,momy tace Allah sarki daughter Allah yadad'a tsareki "kowa ya amsa da amin.

Washe gari dady 'yakira nalam Adamu ,suna cikin wayar ne naji dady yace" yaya so, nakeyi muhad'a Khadija da Humaid aure ,cikin farinciki malam Adamu yace" wanan ai abin murna ne, amma naji dad'i sosai .
Dady ne yace"abinda yasa nakawo wanan shawarar saboda muk'ara k'arfafa zumunci ,malam Adamu yace"karfa kadamu ,sukayi sallama.

"Bayan dady 'yakoma gida yasamu momy da maganar ,itama tayi farinciki sosai sedai tana ganin ,anya Humaid baze wulak'anta Khadija ba ? ".

Saurin kawarda tunanin tayi ,dady da yalura momy tunani takeyi yace" tunanin mekuma kikeyi ,fara'ar dole momy ta k'ir' k'iro tace" duk acikin farinciki ne ".

Yau kawanansu dady biyu da yin maganar auran su Humaid, dady ne yatarasu a parlor'nshi saboda ya gaya musu,halin da 'ake ciki ".

Tunda Humaid yaji wanan kyakyawan albishir ,yadinga farinciki .
Ladidi dajin hakan taji tsoro ya shigeta, saboda tana tunanin,halin da zata shiga ".

Washe gari dady ,yace" ansa biki sati biyu,momy ce tazaro ido tace"sati biyu fa alhaji? dady cikin tuhuma yace "kina nufin yayi kad'an ko¿" eh momy tace.

 Dady ne yace"muyi fatan Allah ya kaimu kawai , Ladidi ce kwance a d'aki tana tunanin halin da tashiga, Allah ma yatemaketa Ammar d'in beyi mata komai ba,tunowa da wayarta tayi kukane ya k'wace mata ,tadinga cewa"wlh nayi nadamar saninka Ammar ".
Bayan sati d'aya ,yau biki saura sati biyu ,momy ce take ta shirya Ladidi musamman takira wata k'awarta daga Maiduguri".

Tunda tazo aka fara yiwa Ladidi dilka dasu magunguna ,tun Ladidi nashan 'na marmari har tadawo k'in maganin,se momy tayi da gaske take sha .
Tadena fita ko da harabar gidan'ne , daga d'aki se sallah ,wani haske Ladidi tayi ,dama fara ce gashi kuma ankuma gyarata.
Tunda akasa biki ango Humaid ya dena zama ,shikuwa Jalal kulum cikin siyayya yake".

Yau biki saura sati d'aya, bak'i ne suka fara zuwa na kusa dana nesa ,Inna hauwa ma ta iso itada malam Adamu ,se dangin momy da suka iso saboda shirye shiryen biki".

A yaune lahadi wata k'awar Ladidi tazo tayi mata make up saboda tanada shago, kwaliyar hausa day akayi mata ,duka k'awayen sunsa" farar riga dakuma zanin atamfa da suka fitar anko ,DJ' Jalal ya d'auko musu ,kasancewa gidan yanada fili ".

Bayan Amarya da ango sun fito ne DJ yace " ga Amarya nan itada angon ta ,please kutafa musu "bayan angama tafinne D J ,ya sake wakar da akayi musu ,Humaid 'da baki yak'i rufuwa ya ruk'o hannun Ladidi suna rawa  ,sauya wak'ar akayi suka nemi guri suka zauna .
DJ ne yace munason muga nera biyar a gurinnan Jalal yaje yasa dubu d'aya, ana cikin haka ne momy ta fito taja Ladidi tace asa musu wak'ar da 'akayi musu ,Ladidi kanta a sunkuye suke rawa da momy ba k'aramin kud'i momy ta zuba ba.

Ana cikin rawa y'an uwan momy suka fitoda ,su goruba magarya taura aduwa se fate wanda yaji kashi a takeaway dakuma dambu ,kai kowa ya yaba wanan shiri da akayi ,anyi taro lpy an tashi .
Washe gari kuma za,ayi ,kumbo day  fans kuzo kuga k'ayatuwa da gurin yayi ,tunda aka fara kumbo ake jiran amarya ,tana can anayimata kwaliya material ne a jikinta me tsada sekuma

head d'in data d'aura kasancewar  milk ne material d'in ,ta d'aura pink head sekuma takalmi shima pink and milk ,woo gaskiya 'amarya tafito sosai ga k'afar tasha lalle ".
Humaid ne yashigo yasa shadda pink hula milk wow shimafa 'angon ya had'u .
Momy da takejin farinciki tashigo da turare a hannunta ta fesawa Ladidi takuma fesawa Humaid sega y'an uwan momy nan sun shigo suna gud'a.....✍️✍️

Mom Islam ce✍️✍️✍️
*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 19_20

______wata kakar su Humaid ce ta shigo tana sanye da wata tsaleliyar atamfa, daka ganta kasan nera tayi kuka sawa tayi aka kirawo Ladidi  ,Ladidi tana kuka 'aka shigo da ita ,lokacin ta canza kaya 'atamfa ce Holland me  tsadar gaske ,riga da skirt ne mai adon stone a jiki ,tunda

'aka fito da ita take kuka mai cin rai y'an uwan momy ne suka rik'ota suka wuce da ita part d'in momy, lulu6eta naga 'anyi daganan kuma 'aka d'auko turaruka masu k'amshi aka fara fesa mata sosai take jin zafin rabuwar ta da iyayen ta gashi kuma yanzu wanda sha'awar ta yakeyi shi za'a 'aura mata  kuma tsanan ta kukan tayi saboda zuciyar ta d'aci take yimata , jiyo muryar mutane suna rangad'a gud'a yasata dawowa daga duniyar tunanin da ta tafi, momy ce ta janyo ta jikin ta kana tace" Khadija duk abinda zance na fad'a miki tun jiya , sai dai zan kuma yimiki tuni da ki rik'e mijinki da 'amana kuma kiyi biyayya 'a gareshi kibi duk wani abu da yakeso inhar bai sa6awa shari'a ba ,wani kukan 'ne yakuma ku6uce mata saboda wanan nasihar ba k'aramin shigar ta sukayi ba ."

Bayan momy ta share hawayen da suka zubo mata tace"wa wasu mata da 'alamu k'annen ta ne tace"musu su raka Khadija d'akin dadyn su , k'afar momy Ladidi ta rik'e tana kuka mai tsuma zuciya ,kowa na gurin saida ya zubda hawaye saboda tausayi, bayan sun kaita d'akin dady ne yafara yimata nasiha bayan wa inda suka rakota sun kauce yafara sanya mata 'albarka daganan yafara  da ina 'alfahari dake Khadija kibi mijinki karkiyi k'ok'arin sa6a mai kuma yakamata kisani karki kasance mai d'aga murya 'akan ta mijinki kibi umarnin mijinki , karki sa6a masa indai umarnin bai sa6awa addinin musulunci ba ,kanta 'a k'asa tace Dady nagode ,wani small box Dady 'ya d'auko wasu  keys ne na mota ,mik'awa Khadija yayi duk da 6acin ran datake ciki saida ta dara saboda tsabar farinciki har k'yal k'yalewa da dariya take,hak'ik'a dady 'yaji matuk'ar farinciki tare dakuma sanya mata 'albarka,kira yayi akan azo a tafi da Khadija ba'adau wani long time ba saiga wasu mata nan suka d'agota kiran sunan dady takeyi amma inna shima baiyi magana ba ,hawayen da suka zubo mai yashere  batare da kowa yagani ba ."

Humaid ne zaune a d'akin abokanan shi yana hutawa ,wani abokin shine yace "abokina wallahi ka huta saboda wanan babyn taka tagama had'a maka komai ,Humaid ne ya gyara zama yana kallon abokin 'nashi yace" banason irin wanan wasan, daga nan ya gyara zama ,jiyo k'arar wayar shi ne yasa shi  duba gurin da ya 'ajiye wayar ,ganin 'number babu suna yasa shi jinkirta d'aukar wayar ,saida 'akayi 6 miss call sanan ya d'auka ,jin muryar wani yasa shi gyara zama k'irjinshi na dukan uku_ uku,ji nayi yace"what!!!. "

Wata razana nniyar k'ara yasa yana cewa no_no wlh ba ita bace kana ya mik'e yana layi ,abokin 'nashi yace "Humaid  akwai problem ne ?" idan Humaid da ya sauya launi ya juyo yace"babu komai zan dawo anjima,abokin baiji dad'in jin hakan ba  'amma sanin halin Humaid yasa shi yin shiru da bakinshi.

Bayan Humaid ya isa gida ne ya hango Khadija ita da k'anwar momy suna magana ,wata muguwar tsanar ta yakeji acikin ranshi, wucewa part d'inshi yayi ba tare da k'ara kallon gurin da 'amaryar tashi take ba?"direct parlorn dady 'ya nufa kafin ya shiga saida ya tsaya sosai yana tunanin kalmar dazai fad'awa dady ,ganin bashiga mafita yasa shi, shigrwa kai tsaye ,bayan yayi sallama ne yasami dady zaune da laptop a hannun shi ,dady ne ya cire farin glass d'in da yake manne a idonshi kana ya juya ya kalli d'an 'nashi ,kan Humaid na k'asa saboda bayason

su had'a ido da dady ,bayan sun gaisa ne dady 'yake cemai lafiya ko naga kayi shiru ?"dady ne ya d'ago kai ganin mood d'in Humaid ya sauya sosai yasashi cewa to me kuma ya faru ?idanun Humaid sunk'ara kad'awa ya d'ago kai yana duban dady 'yace"dady dan Allah dan darajar manzon Allah ka fahimceni ,dady dai baisan inda Humaid ya dosa ba saboda babu abinda ya fahimta ,Humaid ne yace"dady nafasa auran Khadija!!!,sauran kalmar ta mak'ale a bakin shi ganin wani mugun kallo da ,dady ke jifanshi dashi."

Dady da yakejin ranshi yana yimai d'aci ya dubi Humaid 'da jikin shi ke rawa yace"wallahi wallahi ko bayan raina ban yarda 'ace ka fasa 'auran Khadija ba ,da ubanwa yasa kace" kana sonta, kodan kanaso ka wulak'anta mu ?"girgiza kai Humaid yayi saboda yana ganin dady bazai fahimceshi ba  ,dady ne yace"tashi ka ficemin marar kunya da bakasan mutunci ba ni zakazo kacewa wai kafasa 'auran Khadija to dama gobe juma'a 'aure babu fashi wallahi sai anyi ,Humaid ne yayi saurin ficewa daga part d'in dady saboda kar momy tasan halin da 'ake ciki ,komawa bedroom d'inshi yayi ya hau makeken gadonshi juyi yakeyi saboda zuciyar shi ji yakeyi kamar zata fashe , yafara tuno kalar tanadin da yace"zai yiwa Khadija 'amma yanzu gashi komai ya rushe ,yafara kuka kamar k'aramin yaro ,sai kuma ya tuno cewa gobe nefa d'aurin aure dafe kanshi da yake faman ciwo yayi yana salati ,akwatin shi da yacika shi da d'inkuna ya kalla saboda kayak shiki zasukai kala talatin amma gashi komai ya rruguje."

Khadija ce zaune kusa da umma tana k'ara tunatar da ita 'akan zaman lafiya dakuma ibada da hak'uri ,wata gora babba momy ta d'auko tabawa Khadija tace"kinga wanan daga saudiya 'aka kawo min kuma dan ke nasa'aka taho dashi saboda ba ,a ko ina 'ake samunshi ba , ita dai Ladidi ta kasa gane me momy take nufi  ,momy ce ta dubi Ladidi kana tace"zuma ce ta mata kullum zakidinga sha 'amma fa yanada k'arfi,2  small spoon zaki dinga sha ,Ladidi ce take mamakin momy da take zayyane mata maganin mata."

💍 *WEEDING*💍

Yau juma'a yaune dubban jama'a suka shaida  daura auran *KHADIJA MUSA DA HUMAID ADAM*
Akan sadaki dubu d'ari lakadan ba 'ajalan ba 'abokanan su Humaid basu ji dad'in ganin yanayin angon ba kasan cewar baya cikin 'nutsuwar shi saboda 'a inda yake basu labarin shagalin da zasuyi a gun bikin dakuma garar daze kwasa 'amma sunga yanzu ko sunan amaryar baya son ji ."

Kowa ka gan yana cikin farinciki a yau saboda biki yayi biki amma banda mutum biyu wato

Khadija da Humaid , wata k'awar Khadija ce tace yakamata mu tambayi Humaid saboda musan a inda za 'ayi dinner Khadija ce tace"hmm kuna iya zuwa bazan hanaku ba ,babbar k'awar ce mai suna ramsy ta d'aga waya tana lalubar number Humaid 'dan kab k'awayen sunfi shiri sosai ,jin takira wayar tanata ringing ba'a d'aga ba yasata dad'a gwa dawa cikin k'araji yace" wai waye ne please banason takura ,Ramsy ce tace"Humaid baka ganin 'number tane nice fa ,Humaid ne yace"to inna gani sai me yanzu mezan miki hak'ik'a Ramsy taji zafin hakan amma sai ta daure tace"dama maganar dinner ne shine nace kafin a tafi ne za'ayi kokuma sai ankai amarya, jin ya daka mata tsawa yasata zabura tace"daga tambaya saika nemi firgita ni ,to kasani ko a gidan mu babu mai yimin tsawa ka kiyaye ,ko kulata baiyi ba yaja waya ya kashe ,Khadija ko kuka takeyi dama tasan za'ayi hakan ,tafara magana da k'arfi tana cewa"daman wlhi na kawo wanan ranan saboda yaga 'an d'aura 'aure nazama mallakin shi shine ya keson wulak'anta ni."✍✍✍.

*MOM ISLAM CE*✍✍✍..
*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 21_22

____Kashe wayar yayi gaba d'aya dan bayason jin duk wani abu daya shafi Khadija saboda 'a halin yanzu wutar k'iyayyar ta ce take ruruwa 'acikin zuciyar shi, da misalin k'arfe tara na dare saiga motocin angwaye sun zo d'aukar amarya ,bayan angama yimata makeup dasu nasiha 'aka ce tafito su tafi , tunda taji haka ta k'ank'ame momy sosai tanajin zafin tafiyar da za'ayi da ita saboda tayi nadamar auran Humaid amma babu inda zatayi dole ta yarda kodan soyayyar da su momy suka nuna mata gashi dady harda bata mukullin mota,tana cikin tunani ne taji muryar momy na cewa , ina Khadija tayi share hawayen ta tayi kana ta gyara yafa gyalen ta ,jin alamun shigowar umma yasata dai_daita nutsuwar ta , bayan momy ta shigo ta ganta 'a zaune ta takure gefe d'aya , cikin azama tace"taso taso muje kiyi wanka kinga masu mota sun iso."

Jiki babu k'wari Khadija ta tashi ta rufawa momy baya , bayan sun wuce toilet d'in momy ne momy tace "zonan suna shiga momy ta had'a mata wasu turaruka dakuma magun guna ta shige wanka , bayan ta fito ne momy tasa 'ayi mata makeup aka fito mata da kayan dazata sa , fans kuzo kuga Khadija kamar tauraruwa kowa sai mararin ganinta yakeyi, bayan sungama ne aka fito da ita tana sanye da swiss lace mai ruwan ganye ,fito da ita sukayi aka fara rangad'a gud'a Khadija kuka takeyi sosai kamar 'ranta zai fita, momy juyawa tayi saboda bazata iya ganin Khadija 'a yanayin kukan da takeyi ba ,wata kakar su Humaid ce tace" zo yarinya kiyi bismillah ki shiga ,haka Khadija tashige mota tana kuka mai tsuma zuciyar mai saurare , tunda suka tafi momy ta koma bedroom d'inta tana ta sharar hawaye , ganin ai yau ranar farinciki ce a gurinta yasata murmushi da yau Humaid ya auri wacce take so adu'a tayi musu kana ta haura sama gurin dady ,samunshi tayi kwance yana duba wani file na business d'inshi yana ganinta yafara sakin murmushi k'arasawa tayi ta fad'a saman k'irjin shi tana shafa mai kai ,cikin jin d'ad'i dady yace ,lovely na menene ?"🤭momy ce tafashe da kuka tana cewa shikenan yanzu zan dena ganin Khadija 'a kusa dani."

Gyara musu kwanciya dady 'yayi kana yafara share mata hawayen fuskar ta daganan'na rufo musu k'ofa ."

*GIDAN AMARYA KHADIJA*👰.

Zaune take tana ta gurshek'en kuka babbar k'awar ta Ramsy ce tazo kusa da ita tana cewa habba Khady maiyasa saikace ba 'auran soyayya ba ,share hawayen ta tayi batace komai ba ,dan a halin yanzu batajin zata iya wata magana tunda babu mai fahimtar ta, wanka ta sake yi ,kana suka k'ara yi mata make-up wanda yafi na d'azu aka sauya mata kaya zuwa wani material mai laushi suka feshe ta da turaruka masu k'amshi wow koni danaga Khady saida na yarda 'alk'alami na , shirin tafiya suka farayi ai kuwa Khadija na ganin hakan tafara gurshek'en kuka mai tsuma zuciya mai saurare ,zuciyar ta bata gama tsinkewa ba sai lokacin da taga sun yafa mayafi suna shirin fita ,durk'usawa tayi tana cewa kuyi hak'uri ku tafi dani ,nikuwa nace aure fa kikayi hhh yarinya ki gane aure yafi gaban wasa ."

Haka tanaji tana gani suka wuce suka barta ,komawa tayi ta haye makeken gadon ta daya k'awata d'akin, kwanciya tayi can kuma tafara jin tsoro na shigar ta ,misalin 10:pm taji alamun shigowar mota, wani tsoron takuma ji tana 'adu'a 'a cikin zuciyar ta mik'ewa tayi ta lek'a ta window hango shi tayi shi kad'ai yana shirin fitowa daga mota, sanye yake da shadda mai kalar brown wace ta k'ara fito da ainihin kyan shi ,bayan ya rufe motar ne ya d'auko wata leda ya yi hanyar shigowa parlon ,Khadija ce ta koma ta gyara rufe fuskarta da mayafin jikin ta 'takoma tsakiyar gado ta zauna ,da sallama 'a bakinshi ya shigo zama yayi a d'aya daga cikin kujerar d'akin kasancewar bedroom d'in 'nata kujeru biyu ne ammafa sun k'awata d'akin ,bayan ya zauna ne yace"inkinyi ra'ayi zaki iya bud'e fuskarki ,wanan maganar ba k'aramin dukan Khadija tayi ba ,amma batace komai ba ,kuma d'ago kai yayi yakuma cewa to mekuma zaki 6oyemin bayan angama tallarsu a titi ,a firgice ta mik'e tana nuna Humaid 'da yatsa abinda bata ta6a yiba kenan ko musu dasu batayi amma yaukan ya kaita mak'ura ".

Cewa tayi duk abinda ka fad'a 'a kaina nayi shiru ban kulaka ba yanzu kuma ka sake jifana da wanan mumunanr kalmar ?" to wallahi bazan lamunta ba ,kafin ta k'arasa ya wanketa da mari jiki na rawa tace"kozaka kasheni wallahi sai Allah ya sakamin ,wurga mata ledar yayi ya fice a fusace , kwanciya tayi tafara gurshek'en kuka gashi babu mai rarrashin ta.

Misalin k'arfe 11:pm ta mik'e ta daddafa bango saboda mugun ciwon da kanta yakeyi bata gani sosai,toilet 'ta shiga ta wanko bakinta tazo ta zauna tana son cin abinci gashi matsanancin ciwon kai na damunta ,ba'a fushi da 'abinci ,janyo ledar daya wurgo mata tayi tana bud'ewa taga mutuniyar tace wato kaza gasashiya da yogurt aiko tafara yagowa tanaci tana shan yogurt d'in ,duk girman kazar saida tayi rabi ,alokacin'ne taji ciwon kan ya ragu ba kamar da ba ,mik'ewa tayi ta cire kayan jikinta ta sauya izuwa sleeping dress sosai kayan sukayi mata kyau ,bayan tayi adu'ar kwanciya bacci ,tana kwanciya bacci mai nauyi ya tasheta tare da mugayen mafarkai masu firgitar wa, washe gari tunda tayi sallahar asbha ta koma bacci ba ita ta farka ba sai misalin karfe 9:am lokacin ma jin alamun 'nocking d'in k'ofa ne ya tayar da ita".

Zumbulelen hijab d'inta tasa kana ta nufi k'ofa ,tana fita parlor takuma ji ana nocking cikin azama ta isa k'ofar ta bud'e ,ganin yar aikin momy ce yasa Khadija washe baki tace"yaushe kika dawo ne Ummi?"Ummi cikin jin dad'i da tarbar da Khadija tayi mata tace"yau kwanana d'aya ,Khadija ce tace"to kishiga mana kamar bak'uwa ,shiga Ummi tayi bayan ta mik'awa Khadija abincin da momy tabayar akawo musu tuwon shinkafa ne miyar shuwaka wacce taji nama kamar zasuyi magana kai dakaga tuwon kasan zaiyi dad'i ,jere kulolin tayi a dining ta dawo ta zauna ,kusada Ummi ,tambayar ta tashiga yi 'inasu momy da yaya Jalal 'lafiya Lou tace"daganan Khadija ta kunna musu kallo ,Khadija ce ta mik'e tace Ummi ki jirani yanzu zanyi wanka in fito ,Ummi data tuna da kashedin da Momy tayi mata yasata cewa to nimafa tafiya zanyi dan momy na jirana ,badan Khadija taso tafiyar Ummi ba 'amma tayi mata godiya sukayi sallama .

Humaid ne yafito parlor lokacin 11:am na safe sanye yake da wani lallausan yadi mai ruwan coffee kasancewar shi farine ba k'aramin kyau yayi ba ,shafa bak'ar sumar datayi luf a kanshi yayi can kuma ya ciro waya kamar mai jiran wani abu ,Khadija ce tafito tana sanye da doguwar 'riga pink mai adon ston black tayi rolling kanta da mayafin rigar ,tana fitowa Humaid yakai dubanshi gareta cikin zuciyar shi kuwa ji yakeyi kamar yaje yai hugging d'inta tunda matsayin da 'a gurinshi yayi kawai sai ya had'e rai ,ya dubeta tana neman gurin zama yace"keee!!saida gabata ya fad'i tashi ki gyaramin d'akina baki iya gaisuwa bane ?"na iya tace"a tak'aice ,Humaid ne yace "to kullum zaki dinga zuwa gaisheni ko sau goma zan fita kuma in dawo ,to kawai tace" ganin yayi hanyar dining ne yasata k'arawa da gudu ta kwashe kulolin tayi d'akinta dasu ,key tasa ta rufe k'ofar.....✍✍✍.

*~MOM ISLAM CE~*
*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 23_24

______Saida ta tsince naman kaff tukun ta ci tuwon bayan tagama cine ta fito da ragowar parlor, bata lura da mutum a parlorn ba direct ta wuce dining ,saida ta 'ajiye kular ta hango shi yana kan doguwar kujera maicin mutun uku ,zata ruga da gudu ya daka mata tsawa yace"kee!!zonan zataci gaba da tafiya ya mik'e da gudu ya janyota ya wurgata gefe kana yace "wuce ki dafamin dambu,zaro ido tayi kana tace"me kuma mai suna haka?".

" Cewa yayi ubanwa zaki rainawa hankali ¿"cikin jin tsoro da fargaba tace"ni ba rainama hankali zanyi ba ,gani 'nayi ban iya ba shiyasa nake tambayar ka, tsawa yakuma daka mata saida ta tsorata yace"kin zo bariki kin manta da shan garin kwaki ko ?"to kitashi ki goge gidannan kuma kar in dawo insami akasin hakan, haka ta shiga bedroom d'inshi tafara wanke toilet sanan ta dawo gyara bed d'inshi tayo kan TV da sauran kayan kallon ta gogesu kana ta dawo tafara shara tana gamawa tayi mopping, bayan ta gama ne kawai tad'an kishingid'e a gefen bed' d'inshi saboda wata gajiya da tayimata sallama ,bacci ne mai nauyi ya kwasheta 🤭nikuwa nace"anci an k'oshi zaki gane, jin shiru har tayi 1 hour bata fito ba yasashi kashe kallon daya kunna kana ya wuce bedroom, samunta yayi kwance tayi d'ai_ d'ai ,zaro ido yayi kana yafara tunanin irin muguntar da zaiyi mata."

D'auko alurar malaria yayi wacce yake ajiyewa 'a gida saboda koda wata matsalar zata taso, bayan yagama zuba magungunan dayasan Khadija zata bada labari ,komawa yayi kusa da ita

yana k'are mata kallo can kuma yaji muguwar tsanarta tana kuma baiyyana cikin zuciyar shi.

Tunda 'akayi bikin Humaid 'da Khadija babu wanda yayi k'ok'arin kiran su momy gashi yau har kwana biyu da wuni saidai momy na 'aiko da 'abinci kullum ,amma hakan bai sata kwanciyar hankali ba , kiran Jalal tayi a waya yana d'auka tace" dan Allah kazo inason ganinka .

"Cewa yayi momy lafiya dai ko ?"lafiya tace masa daganan ta kashe wayar ba'adau lokaci mai tsayi ba saiga Horn d'in motar Jalal nan kasan cewar baya gida ,yana shigowa tun daga parlor yafara k'walawa momy kira yana cewa momy gani na iso, sako tayi daga matatrakar dake tsakiyar d'akin tace"gidan Humaid nakeson kaje inasan kadubo su ko lafiya ,itadai Khadija nasan batada waya , dariya ce taso ku6ucewa Jalal ganin damuwa k'arara 'a fuskar momy sun kuyar da kansa k'asa yayi kana yace" momy lafiya suke saboda da babu lafiya 'ai dakinji , momy ce ta d'ake tana masifa tana cewa yanzu ka nuna ban isa dakaiba kenan ko?"to walhai tun wuri kaje ka dubomin su kokuwa ranka ya 6aci !!Dady dake saukowa daga bene yace"karka kuskura kaje gidan su , nagaya maka d'ago kai momy tayi tana kallon fuskar dady _dady dake magana cikin bada umarni yace "ka koma gurin aikin ka, to Jalal yace" batare da yakalli k'wayar idon momy ba."

"Momy ce takalli dady can kuma tayi k'asa da murya tace"haba habiby maiyasa kayi hakan?" tana dad'a matsowa kusa dashi , dady ne ya kawar da kai alamun maganar da momy tayi d'azu nazuwan Jalal gidansu Humaid ya 6atamai rai, k'arasawa kusa dashi momy tayi kana tace"haba mana mijina banason fushinka ta kuma marai raice fuska kamar zatayi kuka tace" please afuwan habiby, hugging d'inta dady 'yai tare da janyota jikinshi a lokacin da yake k'ok'arin zama akan d'aya daga cikin kyawawan kujerun,dasuka haska parlorn ,dady ne yake rad'awa momy a kunne yana cemata walhai Aisha saboda salonki dakuma siye zuciyata da kyawawan kalamanki yasa nak'i k'aro aure amma badan hakaba da yanzu matana hud'u .

Tunda ya gama had'a komai ya bud'e mata gefen hanunta jitayi abu na shigarta kamar'ruwa kasancewar ko a hospital ne kowa nason alurar shi saboda batada zafi,haka yayi mata 'alura tana bacci ,jin alamun kamar ana tsikarin ta yasata saurin motsawa, Humaid na ganin haka ya koma parlor saboda karta gane ,tun tanajin abin kad'an har tazo tanajin k'ai k'ayi sosai, inta Sosa k'afa saitaji a kunne inta sosa kunne saitaji a baya ,haka tadinga susa kamar mahaukaciya ganin lamarin yafi k'arfinta yasa tafara ihu tana tsalle tana cewa wayo Yadikko, da gudu ta fice a d'akin tayi d'akinta tana tsalle ,rasa 'abinda yake yimata d'ad'i tayi ganin batada mafita yasata d'auko farar hoda ta cire kayan jikinta duka ta shafe ko ina na jikinta ,ganin abun babu sa'a yasata cewa yaya Humaid!!,
"Kazo ka temakeni walahi narasa inda na kwaso k'ai k'ayi ,shiko Humaid ganin tana magana

tana soshe _soshe yasashi sakin killer small yace" to yanzu mekikeso inyi miki nikuma ?"kije wanda yafara ganin komai ,ya baki magani ,tana susa tace"bangane ba sokakeyi kacemin 'ni mazinaciya ce?!!! menayi ma dahar zaka k'ullamin wanan mummunan sharin oho yace"daganan yabarta tana soshe ssoshe.

Tana kuka tana susa wani gurin har yayi rud'u rud'u tsabar susa tausayin da tabashi ne yasashi shigowa ya mik'o mata magani k'waya biyu yace"ta shanye duka ,babu musu ta k'ar6a tanasha ba'a d'au lokaci masu tsayi ba ,bacci ya kwasheta , said a ya koma d'akinshi yadinga dariya yana k'arawa saboda ya 'ajiye CCTV a bedroom d'inshi kuma bakowane zaisan akwai CCTV a d'akin ba ,kusan k'arfe hud'u na rana ta mik'e had'e da salati a bakin ta ,wata masifaffiyar yunwa takeji mik'ewa tayi ta nufi kitchen tana shiga taji k'amshin indomie jollof ,bud'e murfin tukunyar tayi ganin kayan k'wad'ayin da 'aka samata yasata zaro ido k'wai ne dafaffe sai karas ,abinka da gidan kwad'ayi ai dandanan taji ranta ya biya tuno mai girkin tayi wato Humaid tsaki tayi kana ta sunkuci tukunyar tayi d'aki ,bathroom ta shiga seda tayi wanka tayi brush sanan ta fito ta zauna 'a gaban dressing mirror tana shafa mai tana wak'a tunowa tayi ai bata kulle k'ofa ba ,dagudu ta mik'e taje tasa key tadawo taci gabada Kwaliya bayan ta d'au makeup mai kyau ta ciro shadda bugaggiya mai ruwan coffee tasa takuma ciro bra da pant da warwaro da sark'a wow ba k'aramin kyau tayi ba ,zama tayi gurin tukunyar indomie tafara baiwa cikinta rabonsa saida taci ta k'oshi tayi gyatsa sanan ta mik'e tayi gurin madai daicin fridge d'inta taciro hollondia mai sanyi ta kkora."

Daganan ta 6oye tukunyar .

Yana fita direct kitchen yanufa ganin baiga tukunyar daya d'ora ba yasashi zaro ido had'e da dogon tunani ,komawa parlor yayi ya murd'a handle d'in k'ofar jin a kulle yafara tunanin kodai Khadija ce ta d'aukemai hanyar d'akinta ya nufa jin k'ofar ansa key 'yasashi cewa "wallahi koki bud'emin kokuma duk lokacin da kika fito sainayi maganinki , tanaji yana sababi amma fur tak'i fitowa ,gajiya yayi da tsayuwa , komawa d'akinshi yayi ya watsa ruwa daganan ya fito yayi shirin tafiya gurin cin abinci .

Tanajin k'arar motarshi ta fito rik'e da gyale a hannunta dakuma takalmi mai tsini yiwa drivern gidan "magana tayi da saurinshi ya taho ya durk'usa 'a gabanta yace " hajiya Mota zakishiga ?"eh tace"daganan ta shige mota suka nufi 6ukur park wato anguwarsu momy ,murna take sosai kamar mai shirin tafiya hajji ,suna isowa kusada gate d'in drivern ta yafara horn mai gadi ne yaje ya bud'e mai daganan suka kutsa ciki ,suna sauka ta ruga ciki da gudu,turuss tayi ganin Humaid zaune yanacin farfesu ,zaro ido tayi tana jujuyasu shikwa yiyayi kamar bai ganta ,fakar shi tayi ta shige bedroom d'in momy da gudu ....✍✍✍.

~MOM ISLAM CE~✍.

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 25_26

_____Samun momy tayi ta fito daga wanka ,dagudu taje ta rungume momy saikuma ta fara kuka Momy datake murna saikuma 'annurin fuskarta ya disashe kasancewar taga Khadija na kuka ,janyota momy tayi zuwa bakin gado bayan sun zauna ne "momy take tambayarta tare sukazo da Humaid ne ?" saboda taga Humaid 'din bai dad'e da zuwa ba ,Khadija ce ta share

hawayen ta tace"momy babu komai kawai farincikin ganinki ne ,badan momy ta yarda ba tace"to nima nayi farinciki da ganinki my daughter ,saidai naga kin rame sosai kodai da wata matsalar ne? a'a tace" Momy ce tace"to gyramin gaban mirror d'innan ,to Khadija tace" tafara 'abinda momy ta sata momy tayi hakane domin tasami damar zuwa gurin Humaid saboda shid'in ma ya rame sosai,bayan momy ta fita ne Khadija tace" na shiga uku gara da ban fad'awa momy komai ba da walhi zata iya fushi da Humaid.

"Momy nazuwa parlor tasamu Humaid na danne _danne a waya yana ganin momy 'ya d'ago kai yace" barka da fitowa momyna dafatan kin fito lafiya ? Lafiya lau momy tace"Allah yayi albarka cike da kulawa yace amen momy _momy ce takai dubanta ga Humaid tace"amma dai kuna zaune k'alau ko?"cikin rawar baki yace"eeh eeh lafiya Lou ,momy ce tayi murmushin su na manya tace"bakwa zaune lafiya Humaid a zabure Humaid ya kalli momy 'yace ita Khadijan ce tagaya miki haka ? ko d'aya momy tace"daganan kuma duban Humaid a karo na biyu saboda 'akwai abinda take karanta "cewa tayi karka manta yarinyar nan marainiya ce bamu baka ita dan ka cutar da ita ba kuma na fuskanci ko a lokacin auran kayi farinciki amma metayima dahar zaku dinga cutar da rayuwar ku?" sunkuyar dakai yayi kana yace nikam 'momy saidai kiyi hak'uri dani dan wallahi bazan ta6a son Khadija ba kuma wlhi ko meye ya wanketa zaro ido momy tayi had'e da d'an gutun hawaye tace"ni Humaid kake gayawa wanan kalmar ni ko kukane ya kufcewa momy cikin k'araji tace tunda kazo.duniya bamu ta6a musu dakai ba 'amma zuwa yanzu ne zakace zamudinga musayar yawu dakai ,hak'uri ya shiga bata ganin bata kulashi ba yasa ya durk'usa kan guwaiwar shi yana bata hak'uri,ko kallon shi momy batayi ba ta mik'e cike da matsanancin 6acin rai tace "wallahi wallahi inhar ka cuci Khadija 'Allah ya isa tsakanina dakai!!!."

Cikin firgici ya d'ago kanshi da yayimai nauyi yace "ni momy kike yiwa mugun baki " nafad'a nace nafad'a kozaka mareni ne tunda yanzu ka isa yiwa kanka komai "momy tace" cike da takaicin halin da takeciki, komawa tayi cikin bedroom ta sami Khadija ta zuba uban tagumi girgiza kai momy tayi daganan tace"kitashi kibi mijinki ,Kadija ce ta dubi fuskar momy tace"momy maiya faru naga kamar kuka kikayi ?cikin sasanyar murya momy tace "ba kuka nayi ba kwai raina ne ya 6aci ,adu'a Khadija tayiwa momy daganan ta d'auko mayafinta ta fice, bata sami kowa 'a parlorn ba hakan yabata damar wucewa parking spice da sauri jin anata kiraye _kirayen sallah magrib yasa ta k'walawa drivern daya kawota kira jin shiru bai zoba yasa fara jin haushi tafara cewa kodai'in kar6o keyn mota ta ne?komawa tayi tace" momy bani mukullin motar da dady 'yasiyamin 'nabaki ajiya ,momy ce tace"ina mijinnaki yayi ?"cewa tayi ya tafi wlh kuma driver ba banganshi ba ,d'auko mata momy tayi daganan tayiwa momy sallama ta wuce mota .

Ganin motar a lulu6e yasata yayewa ta shige da bismillah ta fita daga cikin gidan tahau titi ,tafiya takeyi cike da kulawa har Allah yakawota gida lpy, da saukarta ne taga Humaid bai dawo

ba hamdala tayi daganan ta wuce kitchen ta d'ebo kayan shayi duka har indomie kwali biyu ta d'ibo kwai kuma ciko kwali tayi kasancewar yafi k'arfin abin d'ora k'wan a cewarta tadena fita mancewa tayi bata d'auko abin girki ba zuwa tayi tana tunanin da gas da electri wane zata d'auka ,kinkimo gas tayi tana cikin tafiya ne taji alamun dawowar Humaid ,cikin azama ta ruga dashi d'aki tana nishi ,ta rufe k'ofar da key.

Yana shigowa da sallama 'a bakinshi ya doshi k'ofar d'akin Khadija jin ta rufe k'ofar ne yasashi k'wafa yace"wallahi tunda kikaje kika had'ani da momy na wallahi saina miki jina jina ,tana daga d'aki tana yimai gwalo haka yagama sababin shi ya fice ,yayi d'akinshi".

Bayan Khadija tayi sallah taji wata fitinanniyar yunwa na mata sallama mik'ewa tayi ta kuna gas duba tukunyar dazata d'ora ruwan zafi tayi bata gani ba zaro ido tayi tana salati tace yanzu ni mezanci d'anyan k'wai kokuma d'anyar indomie kokuma lifton zanci? babu madara babu sugar ?wayo Allah na nashiga uku ni LADIDI!!.tasa indomie a gaba tayi ta farke leda d'aya tanaci tanashan ruwa kasancewar lemu ya k'are a d'akinta bayan tagama cine tayi ,isha 'I daganan ta haye gado bayan tayi addu'oin dasuka zamemata wajibi ta kwanta badan ta k'oshi ba , asbha ta gari.
Washe gari bayan tayi sallahi ta mik'e tanason fita tanajin tsoro ,shiko gogan tunda yadawo daga masallaci ya zauna ' a parlor ya kunna TV kuma yaune komawar shi gurin aiki wato hospital d'inshi dan tun dare ake ta yimai waya'akan anason ganinshi ,shi burin shi bai wuce yaga ya illata Khadija ba ,ita kuma Khadija tak'i fitowa saboda tsoron Humaid ,gajiya yayi da zama duba 'agogon dake d'aure a tsintsiyar hannunshi yayi ,k'arfe goma da rabi 10:30 bai fita ba duk akan wanan shegiyar yarinyar?"yake tambayar kanshi tsaki yaja ya fice zuwa bedroom d'inshi wanka yayi yana fitowa yaga har sha d'aya tayi 11:am zaro ido yayi ,kamar maijin kashi ,shiri yakeyi jikin gaggawa kamar mai tashi sama da sauri yayi waje gurin motar shi , ya tayar ya mik'i hanya".

Tanajin fitarshi ta fito da gudu tayi d'akin shi ganin kayayyakin daya siyo tayi zaro ido tayi tace"shiyasa ko ya nemi abubuwan dana d'ebo tabb aikuwa saina kwashe wa in an ma ,fara jidowa tayi tana haki ta kwashe kayan abincin dukka harda su carton d'in maltina dana madara dakuma k'wai duka ta kwashe tana dawowa taga wani kayan ganin jikin kwalin anrubuta golden ai kawai ta loda takai d'aki a ranta ko tana cewa shikenan 'na huta da girki ko lemon kwalba ma ya isheni, kitchen taje ta d'auko tukunya da wuk'a dakuma mangyad'a da kayan miya tadawo d'aki tasa key .

Misalin k'arfe biyar na yamma yadawo a gajiye ya shige toilet ya watsa ruwa yana fitowa kwai yaji yana sha'awar shan golden beer zuwa inda ya 'ajijiye kayan yayi ganin baiga komai ba yasashi zaro ido ,cikin kunar 'rai yace "wato wanan tsinanniyar bacin zina har giya takesha?" zama yayi a bakin gado yadinga girgiza k'afa yana bala'i arayuwa bayason a d'auki abinshi ba'a tambayeshi ba ,cikin masifa yafice daga d'akin 'nasa yana zage zage kuma ya kudurta 'a ranshi ko k'ofar zata 6alle yau saiya ci uban Ladidi ,yana zuwa yaji kamar kullum k'ofar a rufe take da key dukan k'ofar yakeyi kamar mahaukaci amma tak'i bud'ewa itako tana tsoron karfa ya 6allah k'ofar nan yazo yakusa kasheta dan yau kamar yasha ya bugu,shigewa cikin drower tayi tanata zaro ido kasancewar akwai gurin sa sak'ata ta ciki kuma tanada zurfi ba lallai mutum ya bud'eta da garaje ba....✍️✍️✍️.

Mom Islam ce

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 27_28

_____Cikin k'arfi ya bigi k'ofar har saida ta bud'e tsayuwa yayi yana maida nunfashi kasancewar k'ofar bata ra'go bace ,kutsa kai yayi cikin d'akin yana haki yana cewa inakike dan ubanki yau saina karyaki ,dube dube yakeyi amma ina baiganta ba bud'e  toilet yayi nanma bata nan rik'e k'ugu yayi kamar mace yanason yaga ta inda zata bullo amma inna ko alamun ta baigani ba, wata muguwar tsawa ya daka, Khadija dake cikin kaya saida ta firgita 'amma dayake tasan tayi lefi ko k'ok'arin guduwa batayi ba , ficewa yayi da gudu yaje ya d'auko wani key a d'akinshi yazo ya kulle k'ofar a tunaninshi ta fice yawo ne, yana fita ta fito.daga ma6oyar ta sai gumi take sharewa ,zuwa gurin kwalayen data d'ibo tayi ganin golden beer dama tasa biyu a fridge ta bud'e ko karantawa batayi ba ta hau sha jin zak'i zak'i yasata lumshe ido ,tanagama sha ta wurgar da gwangwanin ."

Luuu tafara gani wata zabura tayi tafara maganganu tanacewa wai naga kamar duniyar tak'ara haskene tabb naga ta kaina yaukuma gashi goma na dare amma basai ankunna fitillah ba tafara layi tana surutai ,gyatsa tayi tace"sweet lemu kamar nasha zuma kai firig zonan kabud'e in k'ara ,ganin dai fridge bashida niyar zuwa yasata mik'ewa tana layi ta bud'e zata d'auka tafad'i k'asa tana cewa to wane mugunne kuma yake k'ok'arin ganin bayana?"can kuma tasa dariya tace"ni wallahi nagaji da wannan duniyar kuzo ku kaini duniyar ku.

Jin alamun bud'e k'ofa yasata zubawa da gudu yana bud'e k'ofar yad'n matsa yana so ya kamota aikuwa ta fice da gudu tayi kitchen tasa sak'ata lokacin tafara dawowa hayyacin ta ,baibi takan d'akin 'nataba bare yaga 'abinda tasha hannu ya buga'a bango yanacewa kokuma 'ajanun k'auye sun shafeta ne shiyasa take 6acewa?"can kuma ya mik'e yayi d'akinshi jin ana kiran sallahr mgrib , bayan yayi alwala ne ya kulle gidan ta baya ya wuce masallaci ,Khadija najin fitarshi taja jiki tana tafiya tana layi tayi d'aki ,ganin gwangwanin madara yasata bud'ewa ta saida ta shanyeta tass tukun ta kuma kwanta 'a gurin bacci mai nauyi ya d'auketa ...

Jin wani sanyi mai kamada ruwan k'an k'ara ya tashe daga baccin da takeyi duka taji ko ta ina tarasa waye mai dukan 'nata ihu takeyi 'iya k'arfinta 'amma innaa bbu halin tashi bud'e idanuwanta dasukayi mata nauyi tayi ganin Humaid a tsaye kamar wani soja yasata cewa to Allah ya isarmin mugu kawai buge bakin yayi ya cire bell d'in wandinshi yana dukanta ta ko ina ganin babu mai ceton ta yasata juye juye tananeman abinda zata buga mai ,ganin babu komai yasata dai daitar saitin wandonshi ta murd'e gabanshi ta zura da gudu wani wahallalen k'ara yasa mai wuyar fassara wa yarasa maiyakeji ,jiyayi kanshi na juyawa rike da mararshi ya fad'i

k'asa sumamme, Khadija ko kitchen tanufa ta fere doya ta wanke ta dafata daganan ta soya da mai tanayi tanacewa kafin ya tashi naci nak'oshi mugu kawai ,tana gamawa ta soya miyar k'wai kasancewar akwai kayan miya batasha wuyaba seda taci ta k'oshi dak'yar take iya tafiya da ruwan gora 'a hannunta ta k'arasa d'akin ,ganinshi kwance yarik'e gurinda ta murd'e kumfar yawu na zuba 'a bakinshi yasata rugawa d'akinshi da gudu cikin tashin hankali wayarshi tagani a kan gado duba number tahauyi ,ganin doctor Umar yasata danna kira ring d'aya ya d'auka 'a zatonshi Humaid ne ,jin muryar mace yasashi cewa madam barka dai, cikin firgici Khadija tace "Umar dan Allah kazo ka duba Humaid dan Allah kayi sauri ko motsi bayayi ,a tsorace Umar yace " karki damu ganinan zuwa to tace"kawai domin hankalinta yafi na 6arawo tashi.

Ba'a d'au wasu mintuna ba saiga horn d'in motar doctor Umar yana zuwa ya nocking d'aga murya tayi tace"shigo doctor ,da  y'ar jakarshi a rataye ya k'araso yana haki'i tsabar kukan daya ku6ce mata bata iya magana ba nunamai d'akin da Humaid yake kwance tayi , shigewa yayi da sallama Doctor Umar ganin halinda Humaid yake ciki yasashi rik'e kai yana cewa innalilahi wa innailahirraji'un ya Allah help me,idonshi cike da hawaye ya kinkimi Humaid kamar gawa yasa 'a mota cewa Khadija ta kulle gidan ta biyoshi yayi to kawai ta iya cewa kasancewar gani takeyi kamar Humaid ya mutu ne."

Rufawa doctor Umar baya tayi dole ta shige gidan gaba saboda 'an kwantar da Humaid a back side ,tun doctor Umar na hanya yake waya akan a tanadar musu d'akin saboda Humaid babu lafiya kuma yana buk'atar temakon gaggawa kasancewar hospital d'in akwai nisa saida sukayi tayi maid'an 'nisa sannan suka iso a keken tura marar lafiya 'aka turashi direct d'akin da 'aka tanadar musu suka tafi likitoci biyar ne akanshi amma kowa sai share gumi yakeyi ,itako Khadija sai safa da marwa takeyi a harabar asibitin ,likitoci sun shafe wajen awa 1 hour suna bincike akan suma samu nunfashin ya tsaya 'abin ya citura sai da suka kuma shafe mintuna talatin sanan sukayi sa'a ceto rayuwar shi ,ba'amayi batun gurinda 'akayiwa illa ba tukun ganin ya bud'e ido yasa likitocin cewa Alhamdulilh Allah mun gode maka ,jin ana hamdalah yasa Khadija saurin k'arasowa tana kuka tana ganin Humaid ya bud'e ido takama dariya tana yiwa Allah godiya.

Likitocin'ne sukace to yanzu saimu koma kan inda yaketa nunawa tun d'azu a kunyace Khadija ta fice daga d'akin ganin ana k'ok'arin duba gurin bayan sunyi y'an bincike ne suka gano cewar yasami matsala 'agurin kuma indai ba fita dashi k'asar waje akayi ba to kafin yayi sex da matarshi zai iya kaiwa shekarar biyar kokuma k'asa da hakan kasancewar Nigeria basuda cikkakun kayan aiki,kwanansu hud'u a hospital d'in Doctor Umar shike jigila 'akan kayan abinci asibiti dai babu bataun biyan kud'in domin mai asibitinne a kwance babu lafiya.

Yaune aka sallamesu Khadija na tsoron gayawa momy halin da 'ake ciki saboda hukuncin dazai biyo baya ,amma babu inda ta iya dole ta sanar dasu ,tanashirin d'aukar wayane Humaid yace "karki kira su momy dan wallah natashi saina kusa karyaki ,Khadija ce taja baya ta murgud'a mai baki tace a hakanne zaka karyani tabb wlh gara kayi a hankali karka famo gurin da 'akayima bandeji hhh, harararta yayi sanin bazai iya tashi ba yasata fad'ar hakan, rugawa tayi da gudu ta d'auki wayar ta danna number momy ring biyu ta d'auka momy ce tace" my daughter yakike lafiya tace"cankuma tace momy Humaid babu lafiya fa momy ce tace"maiya sameshi ? Shiru tayi can kuma tace" fad'uwa yayi a toilet momy ce tace"to yaji ciwo ne?eh Khadija tace"dan yanzuma 'a kawance yake kwananmu hud'u a asibiti shine yace"wai karna fad'a muku,momy ce tace"to gamunan zuwa 'Allah yakawoku lafiya Khadija tace"daganan ta shige bedroom d'inta ta kwaso kayan abincin datakai can tana cikin kwasowa ne hankalinta yakai kan kwalin golden beer d'inda tasha tana karantawa tahau salati ,can kuma tayi gumm da bakinta mayar da kwalin golden beer d'akin Humaid tayi ta tura 'a k'ark'ashin gado sauran kuma takai kitchen ,wanka tashiga tayi kwaliya kamar maishirin fita anguwa ,shidai Humaid na parlor magana ma ta isheshi ....✍✍✍.

Mom Islam ce

*LADIDIN K'AUYE*

Funny & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 29_30

______Momy ce ita da dady suketa sallama cikin sassanyar murya Humaid yace"wa'alaikumussalam  shifowa sukayi ,ganin Humaid ya mugun ramewa yasa momy k'araswa kusada shi da sauri tace"my son maiya faru dakai naga ka koma haka ?"cewa yayi momy babu komai kwai banida lafiya ne dady daya saki baki yace"to ai Khadija tace "mana zamewa kayi ?" shiru yayi yana tunanin k'arya irinta Khadija cewa yayi eh hakane kasancewar inya fad'a musu halinda suke ciki zai 'iya fuskantar matsala dukda ciwon dayake damunshi , Allah yabada lafiya sukace daganan saiga Khadija ta fito sake baki momy tayi ganin wata uwar 'rama da Khadija tayi amma taja bakinta tayi shiru ,rungume momy Khadija tayi tana murmushi tace "momy na kinzo lafiya ?dady ne yace" to gani a gefe tunda 'an manta dani rufe fuska tayi tace"dady afuwan kunzo lafiya cikin farinciki dady 'yace"lafiya yamai jikin ? dasauk'i tace "cankuma ta shiga damuwa momy ce taga 'alamun fuskarta tace" lafiya Khadija??" fashewa da kuka tayi shidai Humaid na gefe ido ne nashi ,tsagaita kukan tayi kana tace "momy matsala Yaya Humaid yasamu  momy ta bud'e baki tace" a ina?shiru tayi can kuma tace"kuma doctors sunce sai an fitar dashi waje!!! jin wanan kalmar ta k'arshe ya girgiza su momy sukace to matsala yasamu a brain d'inshi?a'a tace" tashi tayi taje ta d'auko file d'in asibitin mik'awa momy tayi ,momy na kar6a ta mik'awa dady Humaid ko dariyace taso kufcemasa wai takasa fad'ar abinda yasameshi hhh,dady na dubawa yace"innalilahi oh Allah momy ce tace"maiya faru ne ?dady daya had'a zufa ba kud'in fita k'asar wajenne damuwar shi ba larurar Humaid d'ince damuwar shi ,dady ne yagawa momy komai dagan suka fara jinjina lamarin.

Dady ne yace ”Allah yakaimu gobe ,dady ne yakira waya airport saboda 'ayimusu tanadin jirgi , yayi sa'a zasu samu na k'arfe 4pm zasubi , dady ne yace ”maganar hospital d'in babu matsala wuyarshi Allah ya kaiku lafiya ,Khadija ce tace ”dady nidai bazanje ba momy ce tamaida dubanta ga Khadija tace ”to ko maiyasa bazaki ba Khadija? "shiru tayi ta sunkuyar dakai ,tana wasada fingers d'inta ,momy ce tace ”aikuwa tafiya dake dole kece matarsa mukuma daga baya zamu biyoku anjima zan sa driver yakawo miki waya saboda gaisawa ,to kawai tace” saboda musu ba halinta bane mik'ewa sukayi suna yiwa Humaid Allah yak'ara lafiya 'amen kawai yace”daganan suka fice ,mita tashiga yi tana cewa mutum bai damu dakaiba baidamu da damuwarka ba baisan darajar kaba 'amma kaje kayimai jinya daga baya 'yazo ya

wulak'antaka,shidai Humaid na jinta bashida lokacin bata 'amsa kasancewar shi ta ciwon jikinshi yakeyi ,wurgamai harara tayi daganan takuma cewa wallahi mukaje ka walak'antani saina k'ara janyo wani jan aikin tunda mutum cin zali yayimai yawa ,zaro ido yayi kuma yana mamakin wai yatsaya wanan shegiyar yarinyar tana gayamai maganganu baid'au mataki ba ,tunawa yayi sai an temakamai zai 'iya tashi k'wafa yayi ya maida kai ya kwanta 'akan kujerar bud'e baki Khadija tayi tace ”da dukana zakayi ahayye ni Dije wallahi kama sameni ne da lokacin da nake garinmu ne tabb dakadinga yimin ladabi dan bana d'aukar 'raini, Humaid maganganun Khadija sun 6atamai rai sosai amma da yanada lafiya babu abinda zaihana ya hukuntata, amma 'akwai lokaci ."

Komawa d'aki tayi tafara had'a kayanta dakuma 'abubuwan dazata buk'ata kitchen ta wuce ta d'ebo naman kaza 'a fridge ta sa kayan k'amshi dasu atta ruhu ta  tafasa naman yana dahuwa ta d'auko turmi tafara dakawa da 'alamu dambun 'nama zatayi bayan tagama ne tahau suya rana gama suya ta d'ibo dakkaken yaji ta zuba 'a roba takai jakar tafiya , d'akin Humaid ta nufa tana duba kaya tana dariya gajerun wanduna ta d'ibar mai sunkai guda ishirin sai t sheet guda goma ,nikwa nace to ina manyan kayan ?" golden beer d'inshi ta d'iba har guda biyar tasa 'a jakarshi ,saikuma man shafawa dakuma takalmanshi tana gamawa ta fice ta nufi d'akinta .

Washe gari misalin k'arfe 9am saiga driver da abincin karyawa dakuma kwalin waya ,tana rawar jiki suka gaisa mik'a mata sak'on yayi godiya tayimai tashige ciki da gudu ,ganin babu Humaid yasata rik'e baki tace ”toshi harya sami sauk'i ne?"batada mai amsa mata tambayarta yasata yin shiru ,tafara duba wayar spark 2 ce maikayau sosai bud'e abincin tayi ganin soyayyen dankali dakuma wainar k'wai a gefe yasata kwashe k'wan tabar dankalin a dining, komawa d'aki tayi tacigaba da shiri wnka tayi ta fifito da kayan data d'ibar musu komawa tayi hanyar d'akin Humaid tana shiga ta hangoshi rik'e da waya 'a hannu da 'alamu charting yakeyi ,girgixa kai tayi tafara cewa lallai to ai basai anje Indian ba tunda kaji sauk'i barin cewa su momy wai abarshi ,da mamaki yake kallonta dubanta yayi 'irin kallon kinrainani d'inan yace”wallah zan 6a66allaki wucemin anan dan ke bata yimiki amfani shine zakimin mugunta ko muguwa kawai dariya tasa tace”kai kadamu da iskanci nikam Allah ya sitiri buk'wai ,shiru yayi ganin raini zai shiga tsakani ,k'arawa gaba tayi tace ”daya d'auka ni yar iska ce ,hmm to ma wai da dayakecemin mazinaciya menene amsar hakan?tana yiwa kanta tambayoyi can kuma tace ”ok natuna lokacin da Ammar ya saceni shine yake zargin 'nice naje d'akinshi?rasa maibata 'amsa tayi hakan yasa takoma d'akinta tana saka sim card a wayar ta memo ta d'auko wanda tayi seven number k'awayenta dakuma ta momy saka numbobin tashiga yi tana murna."

Da misalin k'arfe 3:dai dai dady 'yakira Khadija kasancewar sund'au number tata tana d'agawa dady yace”to inkun kammalah gamu nan a hanyar zuwa airport ku hanzarto angama komai tun

jiya to tace"gamunan zuwa dady ,zuwa d'akin Humaid tayi tace "kafito gasu dady can a hanyar airport mik'ewa yayi jiki babu k'wari yace ina kayana?cewa tayi gasunan a jaka bud'e gurin kayan 'nashi yayi yakuma lodar 'rigada wando kamar yasan bata d'ibarmai ba ,cemata yayi bar 'rawar jiki dan kona sami lafiya 'aure zan k'ara ,Khadija ce tace "a hakan da babu k'arfin jikin kana tafiya kamar mace,zaro ido yayi yace"wlh zanci ubanki shigewa tayi tarabu dashi tasandai koba komai ta gasamai magana.

Shigewa mota sukayi sun d'anyi tafiya sanan suka iso airport d'in samunsu momy sukayi a zaune suna jiransu k'arasawa gurinsu sukayi suka durk'usa suna gaisuwa Humaid dak'yar ya mik'e itako Khadija dariya takeyi k'asa k'asa jin lokacin tafiyarsu yayi yasa momy yimusu fatan 'nasara ta mik'awa Khadija wani babban jaka mai zurfi ,dady ne yace "nayima transfer na kud'i bakada matsalar su godiya yayiwa dady daganan suka shige jirgi ,hawaye Khadija tafara shareware saboda tasan momy ma dauriya kwai takeyi ,jin tashin jirgin yasata rik'o Humaid ta matseshi tsaki yaja yace "dalla ni karki sakamin k'azamin jikinki banza kawai ko kulashi batayi ba tacigaba da rik'eshi ,shikuwa bashida k'arfin kokawa yasa ya k'yaleta....✍️✍️✍️.

Mom Islam ce

*LADIDIN K'AUYE*

Funny & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 31_32

______Suna sauka cikin ikon Allah saiga wani bature yazo yake cemusu  ance yanuna musu masaukin su Humaid saboda rashin yarda yace "saiya kira dady aikuwa yana kira dady 'yace"nine na turoshi dafatan kun sauka lafiya ?lafiya Lou Humaid yace"daganan suka shige motar wanan bature ,itadai Khadija gajiyace ta buwaye ta dan burin ta bai wuce taganta tana hutawa ba ,wani katafaren hotel suka sauka Khadija ce tazaro ido tace"nifa tsoron jajayen fata nakeyi wallahi kar azo angama cinikinmu, Humaid ne ya gimtse dariyar sa shikuwa wanan Bature babu abinda baijiba wanada Khadija tafad'a kasancewar yana mu a mula musulmai sosai amma shi Christen ne saboda baya sallah ,door bell baturen ya danna k'ofar ta bud'e da kanta zaro ido Khadija tayi tace"to Allah gamu gareka tana tafiya tana sambatu shikuwa Humaid ko kallonta baiyi ba ,direct wani rantsatsen step naga sun hau d'aki mai number goma suka shiga ,Humaid ganin ba'ayi maganar komai ga shuwagabanin hotel d'inba yasashi cewa to sukuma masu hotel d'in anbiya sune?eh baturen yace"tun jiya dadynku yayi komai ,godiya Humaid yayimai mutumin 'ne yace"sunanan Joseph barin baka number ta musayar lamba sukayi daganan Joseph yace"suyi wanka su huta za'a kawo musu abinci .

Tana shiga d'akin Humaid ma yashigo tunda tashigo take kallon d'akin kyau tsari gakuma nerorin da 'aka kashemai tabb tace "lallai wasu basusan zafin kud'i ba ,Humaid da gajiya ta tarumai yace"to sannu 'uwarsu zaki 'iya fita ki sanar musu ,ko kallon inda yake batayi ba tashige bathroom wanka tafarayi kasancewar akwai sabon sabulun wanka da sabbin brush da man goge baki saida tayi wanka sanan ta d'auro alwalah tafito ganin har bacci yafara d'aukar Humaid yasata kurma uban ihu tace"wayoo nashiga uku ,a firgice Humaid ya farka yana salati ganin Khadija tayi shuru yasashi cewa komai aka had'a da jaki saiyyaci kara ,zaro ido tayi tace"waye jakin nikake kira da jaki, murmushin takaici tayi tace "d'an adam mai mance hallacci babu komai kasan ba'acin bashina ,mamakinta yakeyi dahar take gayamai maganganu san ranta  saboda taganshi a kwance bazai 'iya 'aikin k'arfi ba yasa takeyimai wulak'anci ,dariya yasa lokaci d'aya kuma yace"yaro baisan wutaba saiya taka."

K'yaleshi tayi tafara sallah tana idarwa ta dubo al qur'anin data taho dashi tafara rera karatu , idon Humaid a lumshe kamar mai bacci ya bud'e ido yana saurarrar karatun Khadija jiyakeyi kamar karta dena ,bayan takammala karatunne ta mik'e tayi gurin kayansu bud'e jakarta tayi ta dubo atamfa rigada skirt mai adon flowers green zatasa kayan ta tuna 'aifa Humaid na d'akin juyawa tayi tace ”malam zaka iya juyawa saboda zansa kaya karkuma 'a kalleni ehe, juyowa Humaid yayi yace”wanan banzan jikin'naki mezan kallah jikinda kowa yagama ganinsa ,tanajin takaicin wanan kalmar amma 'akwai lokacin ramako, d'ibar kayan tayi takoma bathroom ta sanya sanan tazo tana shafa mai kasancewar garin da zafi kuma dukda sanyin  AC mutum gumi yakeyi ,kwaliyarta tayi a nitse sanan wuce dining table d'inda 'aka kawomusu abinci ganin cimar kamar ba irin tata ba yasa ta had'e fuska tana rik'e ciki ,hango wayar tafida gidanka tayi ganin 'number su a calendar yasata d'auka cewa tayi nifa bazan iyacin wanan jagwal gwalon ba 'akawomin tuwo kokuma indomie mutumin da baigane maitake cewa ba yace ” give me one minute please am coming zaro ido tayi tace ”tabb 'banza shima turancin bai gama bakinsa bba."

Humaid daketa dariya yana k'arawa yace”LADIDIN KAUYE y'an mata had'e rai tayi tace”wallahi kabari dan banhuce na d'azu ba, shiru yayi dan yasan komaiye ma zata rina 'aikatawa ,nocking aka farayi Humaid ne ya lala6a ya mik'e saikuma ya tsaya yace ”saikije kiyimai bayani,Khadija ce tace”bagane nawa turancin zaiyi ba  dan 'naga shima koyo yakeyi yanzu hakama brain d'ina tafi tashi ,wucewa kawai Humaid yayi ya bud'e k'ofar mutumin 'ne d'auke da farantin abinci bud'ewa yayi yaga indomie ne aciki godiya yayiwa mutumin daganan yasauka k'asa da tiren abincin samun guri yayi yafara loda indomie saida ya cinye duka sanan ya tashi yabar plet d'in agurin yakoma sama.

Samunta yayi ta rafka uban tagumi tana kuka ko kallon gunda take baiyi ba bare tasanma yaganta taji dad'in 'narkewa bathroom ya wuce yayi alwala yazo ya gabatar da sallah tunda yayi sallama yaketa jero adu'a 'akan Allah yabashi lafiya ,itadai Khadija tarasa meke yimata dad'i a duniya kasancewar bata ragawa ciki ko kad'an mik'ewa tayi taduba maid'an dama dama tafara tuturawa badan yayi mata ba tana gamaci ta d'auki waya takirawo momy cikin farinciki momy tace” daughter dafatan kuna lafiya dai ko?eh muna lafiya Lou "amma momy 'yaushe zakuzo?momy tana murmushi tace”gobe ne insha Allah muna zuwa zamu wuce hospital amma zaku rigamu wucewa,to kawai tace shikuwa Humaid dama can magana ba damunshi tayiba, daganan sukayi sallama da momy.

Dare nayi basuci wani abinci mai nauyi ba ,Humaid na k'ok'arin hayewa gadon  tarigashi ,hak'ura yayi ya koma k'asa ya shinfid'a bargo ya kwanta .

Washe gari bayan sunyi sallahr ashba babu wanda ya koma shirin tafiya 'asibiti sukeyi bayan

Humaid ya fito daga wanka yaduba jakarda Khadija, ta lodamai kaya 'acikin ganin gajerun wanduna yasashi salati yace”wato kinmaidani d'an iska kenan ko ?cigaba tayi da kwaliyarta daganan ta mik'e tana cewa to inka shirya nizan wuce ,Humaid ne yace”kin dad'e baki wuce ba banza kawai jibeta 'ahaka kamar saliha ,shiru tayi saboda batason wanan kalmomin da yake jifanta dashi amma burinta lokacin yazo .

Yana gama shirin ya fice ko magana baiyi mataba jitayi yana kiran Joseph a waya dagudu ta fito tana tsaki ,ganin Humaid yashige mota yasata bud'ewa tashige da sauri wani katafaren hospital suka nufa suna sauka koshi Humaid ' d'in saida ya jinjina kyau irinna asibitin suna zuwa 'aka tarbesu office suka wuce domin ganin babban likitan suna shiga sukaci karo da wani mutumin farine dogo yanada jiki amma ba sosai ba yanada bak'in gashi dakuma gashin baki wanda yafito da tsananin kyawunshi ,kallon Humaid yakeyi kallon a ina nata6a ganinka  Humaid ne yace ”aslamu alaikum mutuminne ya mik'awa Humaid  hannu cankuma mutumin yace”naso nasanka koba kaine Humaid Abdullahi ba ?gingina kai Humaid yayi yace ”nine nima kamar nata6a ganinka 'a lokacin da zamu bud'e hospital d'inmu ,tunani mutumin yayi cankuma yace”ai dadynka abokina ne sosai kuma yayimin bayanin komai toya jikinnaka dasauk'i Humaid yace ”daganan yafara yimai tambayoyi."

Doctor d'inne yakai dubanshi ga Khadija yace” wanan iyalinka ce?  a'a Humaid yace”.
K'anwata ce OK doctor yace ” please zaki iya bamu guri akwai wata magana danakeso muyi maganar ta doki Khadija to kwai tace tafice daga office d'in ,tasami guri ta zauna tana zuba uban tagumi ✍️✍️✍️.

Mom Islam ce

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 33_34

_____Zuciyarta na k'una tarasa maike yimata dad'i amma babu komai ,doctor ne yakai dubanshi ga Humaid yace" yakamata kasani akwai aikin dazamuyi maka kuma yana buk'atar nutsuwarka gaskiya ko kanada mata saidai tayi hak'uri har na tsawo one month kasancewar aikin 'na buk'atar kulawa ,cikin farinciki Humaid yace" doctor ashe zan warke daganan suka fito doctor yanunamai d'akin dazai shiga ,batare da yayiwa Khadija magana ba yashige d'akin yana murmushi 'itako Khadija dataga batada muhimmanci yasata komawa masaukin su zama tayi tadinga rusa kuka kamar wace akayiwa mutuwa ,had'a kayanta tashiga yi tana surutai da alamu ranta ya 6aci sosai ATM d'inshi ta d'auka ta d'auki jakarta tayi waje ,rasa ina zatayi tayi zuciyarta ce take cemata ki koma Nigeria kawai ,hakan ko akayi ta d'auki shawarar zuciyar ta ,mutumin dake jigila dasu wato Joseph shi ta kirawo a waya tacemai dan Allah yazo ya kaita airport ,cemata yayi aisu alhaji suna hanya mezatai a Nigeria ,cikin zak'uwa tace " fils na maganin Humaid aka manta kuma dole saidasu za'ayimai aikin , cemata yayi to bari yakirawo y'an airport d'in yaji ko jirgin 'Nigeria ya tashi, to tacemai dan burinta taganta 'a k'asarta yana kira yacemata nanda 30 minutes sasu tashi ,cikin hanzari taje ta tarkato kayaanta tafito ta kullo d'akin ,barin keys d'in tayi a hotel d'in suka wuce filin jirgi 'itada Joseph ,lokacin da suka isa 'ana kiran Nigeria dagudu tashige kasancewar yanzu harkar Bank akeyi tabiya kud'in komai .

Duba lokaci tayi a ’agogon dake d'aure a hannunta k'arfe 10:23am jin jirgin zai tashi yasata yin adu'a can kuma taji hawaye tafara cewa kuyi hak'uri momy ba'asan raina nadawo ba 'amma babu inda na iya saboda bak'incikin da Humaid ke k'unsamin bayan wasu mintuna ta jirgi ya sauka murna dakuma danasani fall cikin Khadija saboda tana ganin kamar batayiwa su momy adalci ba ,tana sauka tacire sim card d'inta tasai wani wanan kuma tasa 'a jakarta direct gidansu ta wuce wato gidan Humaid ganin mai gadi nanan yasata farinciki nocking tayi had'e da sallama cikin gaggawa mai gadin ya bud'e mata yana cewa hajiya sannunku da dawowa ywwa tace”tashige ciki mai gadin mamaki yafara to ina Humaid d'in??tabb 'bashida mai bashi amsa yasa shi yin shiru, da k'atuwar jaka tafito saboda ta d'ibo kayan abinci su katan d'in indomie dakuma su Maggi star da mangyad'a duka ta loda 'a jakar ,mai gadi naganinta da d'irmemiyar jaka yasashi zaro ido amma babu batun magana ,ficewa tayi batare datace ga inada zataje ba , bank taje taciro kud'i masu ywwa daganan ta dawo gida ,maida jakar tayi tana haki .

*ACAN INDIA*?

Tunda momy suka sauka take gwada number Khadija shiru a kashe ,dady ne yakira Joseph yace”yakaisu hotel d'in da Khadija suka kama d'aki acan ,Joseph da jikinshi yafara sanyi yacewa su dady wanan madam d'in yau tatafi Nigeria, what!!! Dady 'yace”cikin kid'ima ya 'akayi hakan tafaru maikuma yafaru momy da batada wuyar kuka tace”wallahi Humaid ne sanadi dama ba sonta yakeyi ba shine ko rayuwarta ta salwanta bashida matsala ko tana kuka tana magana ,dady ne yace” Joseph muwuce hospital d'in kawai ,mota suka shige suka nufi asibitin da isarsu sunyi sa'a wanan doctorn yanan office d'inshi suka wuce bayan sun gaisa ne sukace ya mara lafiyar yake dasauk'i doctor yabasu amma tare da shada musu d'azu akayi aikin kuma 'akwai alamun nasara masha Allah sukace yanzu ina yake?doctor ne yace” yana room 3 , amma naga bank'ara ganin sister nashi dasukazo d'azu ba ,lokacinne momy tace”matarshi ce doctor ne yace”amma shine yacemin ba iyalinshi ba ,dadyne ya mik'e suka fito dasu momy dakuma doctor room d'in aka nuna musu suka shige."

Ganinshi kwance yana bacci yasa dady dka mai tsawa yace ”ina kakai Khadija?? "arazane ya tashi yace”dady 'yaushe kuka iso ?babu wanda ya kulashi dan haka yayi shiru ,can kuma yace”ai takoma hotel ,dady dayaga Humaid nason raina masa hankali yace ”hotel d'in ubanka !!!...

Momy ce tace ”nidai yanzu damuwata number Khadija kuma gashi a kashe kiran number Jalal sukayi yana gurin aiki yace”bai gantaba rasa yazasuyi sukayi saboda halin marainiyar Allah,  ...

Haka sukayi kwana uku a daddafe duk a tunaninsu Khadija tana gidanta ,a kwana na biyar ne aka sallame su kasancewar Humaid yaji sauk'i sosai gobe zasu dawo Nigeria tunda suka koma hotel d'in Humaid yashiga damuwa dan yasan indai ba'aga Khadija ba to shima ya 6ata dan wallahi saisu momy suncimai mutunci fiyeda tunani, washe sukayi shrin zuwa Nigeria ,jirgin safe sukabi .

*NIGERIA*
Sun sauka lafiya daga saukarsu gidan Humaid suka wuce maigadi ne yace”hajiya fa jiya tabar gidannan saboda naga ta loda kaya 'a wata k'atuwar jaka tashiga motar ta ko magana batayiba ta shige ,momy ce tazaro ido tace”yanzu fargabar da Khadija take jefamu yayi kenan ?" Dady cikin k'unar 'rai yace”kai kuzo muwuce duk inda zataje taje zamatadawo da k'afarta momy na kuka tana kiran sunan Khadija gashi wayarta bata shiga ,Humaid kam yakasa magana dan yasan kad'an suke jira sufara balbaleshi da masifa  'a motar Humaid suka wuce can anguwarsu momy suna sauka Jalal na shigowa yana ganinsu yace”ina Khadija fa momy ce tashige ciki da 'alamu kukanne zai ku6ce mata shikuwa dady cewa yayi ta 6ata ,Jalal daya tsaya kamar gunki yarasa takamai man amsa yace ”to nikam yaya Humaid ina Khadija? "wani mugun kallo Humaid yayiwa Jalal daganan yashige ciki.

Damuwa iya damuwa sun shiga sosai amma shi Humaid bai damu sosai ba kasancewar ba damuwarshi bace ,dady dayaga abin babba ne dan yau da dawowarsu kwana uku yacewa su momy su shirya suje k'auye ko tana can ,momy batayi wata kwaliya sosai ba ta fito suka wuce itada dady ...

Da isarsu malam Adamu yafara yimusu lale marhabun shigewa gidan sukayi suka sami 'inna tana zaune tayi k'wad'on rama ,zubo musu tayi aka kawo musu ruwa mai sanyi na randar k'asa ,malam Adamu ne yace”ina zuwa can anjima saigashi yadawo da k'waryar fura da nono dakuma ludaya ,zuzubawa su momy akayi bayan sunci sun k'oshi sukace dama 'abinda yakawomu shine mund'auka Khadija tazo nanne?"inna dake cin rama tace”walhi rabona da ita tunda 'akayi bikinsu nikam mukuma bamu k'ara wai wayarku ba malam Adamu ne yace”to yar

marainiyar Allah ina tashiga momy ce tace”har wayarta sun gwada amma 'a kashe ,shirin komawa sukayi dady 'yabawa malam Adamu dubu hamsin sukayi gaba,godiya su inna suka dinga jerowa suka yimusu rakiya,har zuwa gurinda sukayi parking d'in motarsu.

Dady 'yana tuk'i yana tunani anya ba wani abin Humaid yayiwa Khadija ba dan sunsan halinta batada son zuciya ,momy ma 'a tata zuciyar tunani takeyi kodai Humaid ya cusa mata wani mugun abunne yasata guduwa ,har suka bar garin babu maiyiwa wani magana,da isarsu jos suka wuce gidan TV da gidan redio domin bada sanarwa ko 6ata tayi ...✍️✍️✍️.

Mom Islam ce

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 35_36

_____Daganan sukayi gida jiki babu k'wari kowa ya sauka 6atan Khadija yazame musu tamakar mutuwa tayi ,dady ne yakira Humaid a waya yake cemai maza _maza yazo yanason ganinshi ,gaban Humaid na fad'uwa ya shigo gidan bayan yayi parking d'in motarshi ne ya shiga parlor ganin babu kowa yasashi wucewa d'akin dady ,samun dady 'yayi a kishingid'e kamar mai bacci, da sallama ya shiga yanemi guri ya zauna zaice ina wuni dady, _dady 'yace"bana buk'atar gaisuwar ka saboda yanzu batada 'amfani kuma wallahi kaje ka nemomin Khadija duk inda tashiga kokuwa kayi danasani a rayuwarka ,gumi ne yafar a keto mai tako ina yace"dady nimafa wallahi...wani azabbaben mari dayaji saida ya mik'e yana shirin bigewa da bango ,ficewa yayi daga gidan yana gunguni ,shima Humaid d'in gidan TV da gidan redio ya nufa yabada cigiya daganan yakoma gida yana 'adu'oi akan Allah ya baiyyana ta yafita daga masifar da iyayenshi suka kirari ,yaukam hankalinshi ya tashi sosai ganin fushin dady ba k'aramin tsorata yayi ba .

Washe gari ko gigin zuwa gidansu baiyi ba kasancewar bayason jin kalmomin da zasu hargitsamai k'wak'walwa , gashi yau saura sati d'aya ciwon jikinshi ta warke ,kuma yanada burin yin aure domin 6arje sabon shafi ,amma baisan wazai tunkara da maganar ba tunda wanan muguwar ta gudu ai ta jazamai fitina ,kwata_kwata bashida kwanciyar hankali kamar shine marar gata 'a duniya 'amma yasan mafita k'auye ya nufa gidansu malam Adamu yana shiga yasamesu suna ,zaune shida inna bayan ya gaishesu ne yake yimusu jajen 6atan Khadija ,malam Adamu ne yace"yau kimanin sati uku kenan Allah yasa tana raye ,amen yace "can kuma yace"dan Allah baba inaneman wata 'alfarma ne ,babane ya maida hankalinsa ga Humaid yace" inajinka yaron kirki maiya faru ?"sunkuyar da kai Humaid yayi yace" baba sonakeyi nayi aure kafin Allah ya baiyyana Khadija muci gaba dayi mata 'adu'a."

Jinjina kai malam Adamu yayi saboda lamarin babu dad'i wato shi ta 'aure ma yakeyi ,cankuma yace" karka damu yarona yaushe iyayen ita yarinyar sukace ka turo ?"cikin rawar jiki Humaid yace" ranar juma'a ne ,malam Adamu ne yayi lissafi yace" saura kwana hud'u kenan to insha Allah zanzo kuma kafin inzo zankira mahaifinnaka muyi magana ta waya ,inna ko sai jinjina kai takeyi tana tuno Khadija, godiya Humaid yayi tsabar farinciki bandir d'in y'an dubu ya 'ajiye masa yana komawa mota ,yakira budurwar tashi saida sukayi hira sosai sanan sukayi sallama , ya mik'i hanya tafiya yakeyi cikin farinciki da nishad'i saboda yakusa zama 'ango hhhh...

Tunda yakoma gida ya kirawo masu decorection d'in gida gyra 'aka yiwa gidan kasancewar yarinyar y'ar manya ce shiyasa yakeson shima 'asan d'an manya ne ,part d'inta na can gefe gaban d'akin Khadija kayan Khadija kuma 'yadawo dasu k'asa 'amarya takoma sama ,kwana uku da magana ,dama Humaid ko k'ok'arin dosar gidan baiyi ba ,momy dajin zancen auran Humaid batace uffan ba haka shima dady 'yace" babu hannunshi ,malam adamu ne sukaje gidan surukan shida Humaid shikuma Humaid ya wuce gurin budurwar sa mai suna khairat ,hira sukeyi cikin so da k'auna dama irinta ya dad'e yana nema wato mai budadd'en ido ,ruk'omai hannu tayi tace"zomuje zagayeshi tadingayi da girma dakuma shuke shuken gidan suna rik'e da hannun juna....

Malam Adamu na fitowa ya koma can gidansu dady baisami dady a d'akinshiba yasa ya danna number Humaid, yana d'agawa malam Adamu yace" to kazo anyanke magana ,cikin azama Humaid yabaro gidan yayo gidan su ,samun malam Adamu dayayi shi kad'ai yaji dad'i sosai ,malam adamu ne yace" sun yake dukiyar aure nabada cikin kud'in da kabani d'azu to ansa biki sati uku masu zuwa ,godiya Humaid yaketa yimai daganan malam Adamu yace" zai koma, wasu mahaukatan kud'i Humaid ya d'ibo yabawa baba ragewa yayi kana yace" Allah yasa 'albarka saganan sukafice ,Humaid da sauri yafice daga gidan kamar marar gaskiya hmm..

Da kanshi yaje ya had'o kayan akwati daganan ya zarce gidan mahaifiyar momy yabata labarin abinda yafaru da Khadija amma yad'an had'a da k'arya ,su hajiya lefinsu dady suka dinga gani kuma sukace insha Allah zasu tsayamai kan maganar auran ,godiya yayi musu yabar kayan a gidan yadawo gidanshi ...

Yau saura sati biyu biki shirye²akeyi ta kowane 6angare amarya kuwa gyara takesha kamar ba gobe ,batun soyayya kuma sai abinda yayi gaba dan babu baya, ana biki saura 1 week ne dangin momy suka kai kayan akwati ,da shigarsu dangin maman khairat suka hau gulma suna cewa ji wanan banzan akwatin kamar na y'ar talaka ko besan wa ya 'aura bane?,sudai dangin momy haka suka kai kaya suka dawo jiki a sanyaye, dady ne yakira Humaid a waya yake cemai duk wasu takkaddu dayasani na hospital d'inshi to ya tarkato ya kawomai dan haka shima tuna 'aure zaiyi yafara neman 'nakanshi tashin hankali gamida rikicewa Humaid yashiga ko 6atan Khadija baisashi shiga damuwa irinta yauba ,hak'uri yake bawa dady amma ina dady 'yace" aina rantse ,daganan dady 'ya katse wayar ....

Yau saura kwana biyu d'aurin aure Humaid yayi d'inkuna sunkai kalla goma saboda murnar khairat ,a yaune dady 'yabada saukar alkur'ani mai girma masallatai akan 6atan Khadija , Humaid ne ya tattarawa dady kayanshi ya kaimai ,dady ko kallonshi baiyiba shikuwa Humaid

mamakin abinda dady 'yayimai yakeyi ,kiran Jalal yayi a waya yake fad'amai halinda yake ciki ,Jalal cikin k'unar'rai yace "to Allah ya kayauta nikam ina goyon bayan dady kasancewar baka damu da Khadija ba,Humaid ne yaja waya ya kashe saboda 6acinran yafara isarsa."

Washe gari akayi dinner anzubar da kud'i a bikinnan ,Humaid ko tunaninshi in kud'inshi suka k'are ina zaisami wasu ?amma bashida 'amsa gashi yarinyar sai k'irk'iro hidimomi takeyi kuma bayason yin harkar k'aranta hmm ,momy kam tamik'wa 'Allah komai ganin Khadija batada niyar dawowa gashi yau watanta biyu bata gida 'Allah yasa dai tanacikin k'oshin lafiya .

*WEEDING💖💫*

Yaune dubban jama'a suka shaida d'aurin auran Humaid ADAM da 'amaryarsa KHAIRAT USMAN DOLLARS akan sadaki dubu d'ari biyar hmm tofa riders kunjifa 😉,kowa mamakin kud'in auranan yakeyi amma babu mai bakin mgna kasancewar gaba da baya securitys ne kewaye da gurin ,y'ar manya kenan,misalin k'arfe 9pm aka wuce da ita gidanta ,duk iskancin su saida suka yaba da gidan saboda ba k'aramin kyau yayi ba misalin k'arfe 10pm kowa ya watse daga 'amarya sai ango ,bayan sunyi sallah ne ya dafa anta yayi mata 'adu'a daganan aka faracin kaji ,bayan sun kammalah ne Humaid yashige wanka 'a can toilet d'in shi itama 'amaryar wanka tashiga ta sanya sleeping dress.....✍✍✍.

Mom Islam ce

*LADIDIN  K'AUYE*

Funny  & love story.

*Labari mai ban dariya had'i da fad'a karwa*

*NA*

*MOM ISLAM*
*ZAINAB HABIB*

*MARUBUCIYAR:*

*ZAINABU ABU*

*AND NOW*

*LADIDIN K'AUYE*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

*Episode:* 37_38

______Da sallama yashigo yana sanye da gajeren wando ,ganinta 'a kwance kan gadon yasashi rungumo ta ,itako amarya jin haka yasata fara kissing Humaid cikin zumud'i humaid dai rasa kuzarinshi yayi saboda Khairat na neman sauya salon izuwa cire kayanta ,humaid ko mamakin inda khairat bata tsoron wanan dare yakeyi saboda yaji ance duk mace na tsoronsa, mirginawa gefe yayi yana maida nunfashi khairat kuwa haushi yabata dan ita bataso hakan ba ,Humaid zai mik'e takuma taroshi tace "wallahi baka isaba kamance da hakk'ina daya rataya a wuyanka?"shiru Humaid yayi can kuma yakoma gurinta ,kasancewar itace jigon abin yasa baisha wuyar samun hanya ba ,ko jigata sosai batayi ba ,lokacinne Humaid yafara sambatu yana shimata 'albarka kasancewar tana tareda budurcin ta ,bayan yasami nutsuwane ya sauka 'aikuwa yana sauka ta matsoshi ,cewa yayi wanka zanyi na kwanta lokaci yayi nisa, zaro ido Humaid yayi yace"to ai saimu kwanta amma yanzu tashi muje muyi wanka ,mak'e kafad'a tayi tace "wallahi ni bai 'isheni ba 😒garama kadawo ,ficewa yayi ko kallinta baiyi ba itako Khairat kuka tafara tanacewa namiji kamar mace babu kuzari wallahi saina gyaraka.

Tunda Humaid yakoma d'aki yafara tunanin ko.Khairat na daga cikin wa inda' ake cemusu harijai ne shifa bazai 'iya yin abu kullum ba kamar abincin gida ,ya shige wanka ,6angaren Khairat kuwa lokacinne takumajin wata sabuwar sha'awa na tasomata zabura tayi ta mik'e tafito part d'in Humaid ,ganin k'ofar a bud'e yasata shigewa batare datayi sallama ba ,cire kayan jikinta tayi ta kwnta d'ai d'ai tana jiran shigowar  Humaid ,Humaid yaga lokacin datashigo

yasashi k'in fitowa daga bayi ,yanemi guri ya zauna kamar zaiyi kuka, itako gajiya datayi da jiranshi yasata batasan lokacinda bacci mai nauyi yayi gaba da itaba ,yana ganin tayi bacci ya fice kamar munafiki cikin sand'a ,parlour yakoma ya kwanta.

*WASHE GARI*🤙
Washe gari kowannen su yatashi yayi sallah shiko humaid masallaci ya wuce saida gari yayi haske sanan yadawo gida, yana shigowa ya tarar da khairat da fara'arta tazo dagudu ta rungume shi ,shima fara'a yayi mata daganan tajashi zuwa dining, k'arewa kwaliyarta kallo yakeyi dan ba k'aramin kyau tayiba ,sanye take cikin riga doguwa ta shadda mai ruwan pink 'suna isa dining ta bud'e wani food flaks mai shegen kyau ,humaid ne yace "wanan kuma daga Ina "tana murmishi tace "daga gidan momy na ,masha 'Allah yace Allah yabasu lada 'amen khairat 'tace "daganan tafara saving d'inshi tana bashi a baki ,farinciki fall zuciyar humaid yana cewa yanzufa nayi aure ,aini 6atan khadija yayimin rana tabb da tanan babu maibarina inyi aure ,shima bata'a baki yashiga yi saida suka k'oshi tukun khairat ta taso daga chair d'in datake zaune ta haye jikin humaid ,wasu abubuwa takeyi mai masu wuyar fasarawa abinka da farin shiga dan danan yafara sauya sallo ,kinkimarta yayi sukayi bedroom d'inshi ,ya shafe minti hamsin suna 'abu d'aya."

6angaren su Jalal kuwa soyayya suke zubawa wacce babu algus kowa bayason yaji 6acin ran d'an uwansa shiri takeyi zatace hospital gaishe da Khadija da ake yimata k'arin ruwa Jalal ne yace ”Honey inkin gama kizo mutafi ,shagwa6e fuska tayi tace ”anya babyn ma zaibari na fita kuwa ,k'arasowa Jalal yai dai _dai saitin cikin nata da zaiyi wata hudu ya kasa kunenshi yana dariya ,girgiza kai yayi yace ”to baby's sunce ko America zaki saikin dawo ,dukan wasa ta kaimai tana cewa tabb barinzodai mu tafi dan naji ance jikinata yayi tsanani ."

Emergency room aka kwantar da ita saboda lokacin da ta yanke jiki ta fad'i Allah yasa da mutane a gefe ,kwance take ansa mata oxygen wato abin nunfashi ,nunfashinta baya fita sosai kowa ya cire rai da khadija momy kuwa sarkin kuka kullum cikinsa take tanacewa kukuma jarabawarku kenan wayo rayuwa, Saudat ce tayi sallama ita da Jalal amsawa su momy sukayi itada k'anwarta  durk'usawa har kasa sukayi suka gaidasu momy dagan an ya ajiye food folks a gefe yace "ya jikin Khadijan da sauki momy tace ”had'a baki sukayi gurin cewa Allah yabata lafiya amen momy tace ”bayan Jalal ya zauna ne yace ”momy number ya Humaid bata shiga yau 3 days kenan ina gwadawa amma a kashe ,momy ce ta share hawayen da suka zubo mata tace ”shima dajin wanan lamarin da yafaru a gidannasu ya kwanta rashin lpy dan naji ance jikin ya tsananta sosai ,Jalal ne ya tausayawa yayan nashi yace ” momy insha Allah jibi zantafi dubo shi to Allah ya kaimu tace ”daganan shiru ya biyo baya."

Momy ce ta shiga room d'inda aka kwantar da Khadija samunta tayi ido a kakkafe tana kuka momy tsabar firgici tayi gurin doctor tana kuka ,da sauri doctor Umar ya shigo yafara gawaje gwaje ,cikin sa'a nunfashin ta ya dawo normal can tafara bud'e ido ruk'o hanunta momy tayi tace ”alhamdulilh daughter Allah yakara miki lafiya ,Khadija babu bakin magana sai kalle kalle takeyi..

Tabarmai nagani da mutane a k'ofar gidansu dady kowa kaganin fuskarsa bbu dad'i zaman makoki akeyi dakuma adu'oi , dady ne keta kar6ar gaisuwa gurin jama'a suna yimasa ya karin hakuri ,washe gari jikin Khadija yayi kyau sosai dan har tana cin abinci sosai ,sallama aka basu suka wuce gida ,Khadija na ganin yan zaman makoki tafara tambayar waye ya rasu ,momy ce ta tuno da sharud'an da doctor ya gaya mata akan ta kiyayen 6acin ranta kokuma shiga damuwa ko gani ko jin fargaba ,momy ce tace ”suna hutawa ne kinsan wanan watan dolle sai anyi meeting da ma'ai kata ta gamsu da baya nin momy shiyasa ma bata k'ara d'aga hankalinta ba....

Kai nimafa mom Islam abin ya d'auremin kai 😢meya faru a gidansu Khadija ??waye ya rasu ??? tabb todai kubiyoni danjin inda muka dosa👏.

Kwance take tana wani matsanancin kuka  rabonta da abincin kirki tun da wanan abin ya faru ,tarasa ina zatasa kanta gashi Allah ya jarabeta da abubuwa duka biyu ,alwalah ta d'auro tazo tafara nafilfili tana gayawa Allah damuwarta ,washe gari yaune akayi sadakar uku mutane sun ragu sosai ba kamar daba ."

Kale ² takeyi a d'akin tarasa meyafaru bazata iya tunowa ba ihu tafarayi dan razana take koda wane lokaci ,momy da tatashi akan darduma tayo d'akin da gudu ta sami Khadija nata juya kai tana ihu ,wasu zafafan hawayene suka zubowa momy tayi waje da sauri ,driver ta k'walawa kira cikin azama yazo ya drk'usa a gaban momy _momy ce tace "maza ka fito da mota mu koma hospital  ,komawa tayi ta ruk'o Khadija tafito da ita hijab d'inta ta Sanya mata daganan sukayi mota ,dak'ayar momy ta sata a mota suka wuce hospital, sunyi sa'ar ganin doctor ,inda yake sanar musu cewar su dage da adu'a kuma akwai abinda take tunawa yake tsorata ta magunguna ya kuma basu yace "ku kulla sosai da ganin tasha magani."

Haka driver ya dawo dasu gida ,matane keta shigowa gidan momy suna yimata ya karin hakuri ,wanan su shigo wanan su fita dayake momyn ta mutane ce .

*KAUYE*
Sahura ce ta shigo gidan inna da gudu tana shewa ,had'e fuska inna tayi tace "fitarmin a gida nace kifice ko ,dariya Sahura tasa tace " inna ya alelen ranan waya biya kud'in ¿"ubanki ne ya biya kinji ,sahura ce ta zaro ido tace " ubana fa sirikinki ne ,inna ce ta d'auko sanda tana shirin buga mata wani yaro yai sallama yace " Aslamu alaikum zakusi kai da kafar kaza ?" tsalle Sahura ta doka tace "kai yaro kawo nan shigowa yaron yayi ya nemi guri ya zauna ,Sahura ce ta dubi inna tace " hmm sai na tuna lokacin da mukaje gidansu Ladidi kullum sai naci kaza ,amma yauma Allah yasa inada ragowar kud'in da Humaidu ya bani d'ari biyu na siya ,dajin haka inna ta washe hak'ora tana dariya tace "yoo ai siyama zakiyi koda na d'ari ne Sahura ce ta tambayi yaron nawa nawa ashirin ashirin yaron yace "kasiyar uku hamsin ¿"eh kawo .

Kai ta d'iba guda biyu k'afa kuma d'aya duban inna tayi data zuba tagumi tace "toke bazaki d'auka bane ?inna ce tace "to masu abin basuce in d'auka ba ni na isa ,dariya Sahura tasa tace "laaa ina ki d'auki na hamsin ,inna na sid'ar hannu ta d'auka harda zubo romo ,yaron yana zaune har suka gama ci Sahura tace "ga hamsin d'inka kajira wanan tsohuwar ta baka kud'inta inna na sud'e hannu tace "kan uban ke kin biya naki hakafa kikayimin ranar sai malam ne ya biya yana fad'a Sahura dake taunar k'ashi tace " maganin mai kwad'ayi komai mutum saiyyaci ,inna ce ta kunto zaninta gudar d'ari biyar ce a jiki mik'a wa mai kai da k'afa tayi tace "k'aromin na hamsin ,dan ubanta ni zata rainawa hankali*LADIDIN KAUYE*

funny & love story

51_52

Yaro dai na ganin ikon Allah ya je ya samo canji ya kawowa Inna ,Sahura ce tace ”au kewai inna kina gadarar zaki bani haushi ne aikin 6urr saidai inbaki haushi ta ja gyalena ta d'aura a kwankwaso ta fizge kwanon da inna tasa a dad'o mata naman ta ruga da gudu ,kuka inna tasa tana tsinewa Sahura tana cewa ,shegiya ga kashe d'ari danayi tashi d'aya gashi iya romo na tsaya sud'a ta wafce kwanon ,shidai mai talla gaba yai yabar inna tanata surutunta."

_JOS_

da sallama ya shigo yana cewa momy yau akayi sadakar bkwai to Allah ya gafarta masa kuka momy takeyi sbda inta tuno abinda yafaru amma aikin gama ya gama rayuwar batajin dad'in yinta sbda Khadija har yanzu sai sauk'in Allah yanzu ciwon 'nata ya koma kamar na mai aljanu in ciwon ya tashi to guduwa take burin yi dady abubuwa sunyi mai ywwa sosai duka dai familyn gidan basuda wal wala ,kwance take tana bacci sai kuka takeyi kuma da k'arfi ,momy ce ta shigo d'akin ta sameta tana bacci kuma tana kuka ,adu'oi tashiga yimata tana tofa mata ,yunk'urowa tayi tana gurnani zata hankad'e momy ,cin sallamar Jalal yasa momy k'wala masa kira ,da sauri ya shigo yana cewa momy lafiya kuwa ¿inafa lafiya Jalal ?narasa yaza’ayi da ciwon Khadija kullum abin baya lafawa kullum cikin fad'a muke gashi banda kunu batacin komai y'an aikin gidan suntafi garinsu ,sai kuma tasa wani kuka mai ban tausayi ,hak'ik'a momy mace ce wace batada zalunci batada mugunta kuma bata fifita wani akan wani ,Jalal shima abin yafara damunshi kukan da momy keyi ya kuma tayarmai da hankali ,sukan sunga jarabawa Allah yasa su cinyeta duka."

Washe gari antashi da wani sanyi mai shiga mai shiga jiki tunda gari ya waye khadija keta ihu tana k'ok'arin fitowa wani girgiza d'akin yakeyi ga wasu k'ara dake baiyyana a cikin d'akin ihu takeyi iya k'arfinta ,dady daya shigo yanzu yai d'akin da sauri ,ganin inda jikin khadija keta 6ari yana makyar kyata yasashi cire hular kanshi adu'oi yaketa karanto mata amma sauki sai lokacin da Allah ya nufa ,gefenta wasu abubuwa take gani masu ban tsoro sai nuni take yiwa dady ina shikam bai gani ba ,ihu take kuma yi tana ruk'o hannunshi amma dady babu abinda yagani yarasa wane ciwo ne ke damun khadija , adu oin da yai mata yasamu jikin ya lafa dan har bacci ya d'auketa."

D'akin momy ya nufa zaune ya sameta kan sallahya tana azkar shigowar sa ne yasata shafa adu'a tace ” barka da dawowa mijin kirki ,dady ne ya fitar da wata zazzafar iska daga bakinshi ya d'aga hannu sama yana cewa Allah mun gode da jarabawar da kayi mana Allah ka kawo

mana mafita ba yawan arzik'inmu ba bakuma yawan ibadunmu ba Allah ka dubemu ,suka shafa tare da cewa amen.

Wata girgiza sukaji mai firgitarwa momy zata tashi dan taga meke faruwa dady ya tsayar da ita yana cewa kibari in lek'a ,momy na shirin kuka tace "gaskiya sai dai muje tare ,hannun dady ta rik'e tana kuka suka fita , duk wanan hayaniyar da girgizar duk a part d'in Khadija yake faruwa hatta k'ofar ma girgiza takeyi kuma a bud'e take ,dady na shirin lek'awa momy ta rik'oshi tace muje mu nemo malamai dan Allah ,hankalin dady a tashe damu warshi wane hali baiwar Allah take ciki marainiya ,kutsa kai yayi momy na tsaye ya wuce ,kwance ya sameta d'akinta duk ruwa mai had'e da jan abu mai kamada jini sai wasu surutai takeyi ,kafin dady yace "bismillah kawai aka d'aukeshi aka gwara da jikin bango ,ihu momy takeyi iya k'arfinta gadai khadija a kwance shikuma dady ,kowaye yayi mai haka oho , mai gadi ne da driver sukayo cikin gidan a tsorace ,momy babu magana sabda kuka yaci k'arfinta saidai nuni da hannu ,hango dady sukayi a mak'ale a jikin bango shi bai sauka ba shikuma bai yi sama ba, wani hayaki ne ke fitowa amma Khadija na kwance tana bacci ,driver ne yace "anya babu shed'anu a lamarin kafin ya rufe baki yaji an wankamai mari ,ganin basuga kowaba yasa mai gadin da driver da momy suka arce da gudu , d'akinta momy ta koma ta d'auko wayarta ta kirawo Jalal ring d'aya ya d'aga yana sallam momy ko amsawa batayi tace "Jalal.ka kirawo mai ruqyya dan Allah dadynku tana kuka to yace kashe wayar momy tayi tana adu ar datazo daga bakinta , bayan 30minutes sai gashinan shida wani babban malami sun shigo ."

Gai sawa sukayi da momy daganan tayimai bayanin ciwon Khadija dakuma halin da dady yake ciki ,ruwa ya buk'ata domin alwalah bayan ya idar da alwalar ne yace "a nunamai d'akin ,momy ce ta shige gaba itada Jalal shikuma malamin na baya da Qur'ani a hannunshi ,da hannu momy tayimasa nuni da d'akin ,lek'awa yayi ya hango dady jingine a jikin bango shi baya k'asa auxubillahi yace " a lokacin da yake karanta suratul bak'ara ,jikin dady ne ke jijiga yana wani gurnani tsananta adu'a malamin yayi , Allah cikin ikonsa saiga dady ya fad'o yana tangad'i ,malamin ne yace "asamu yayi wanka kuma ya kwanta ,kan Khadija aka koma daketa bacci ko motsi batayi adu'oli iri _iri malamin yayi amma har yanzu shiru ,d'akin sai fitarda wani hayak'i takeyi mai ban tsoro."

Fitowa malamin yayi yana yarfe gumi yace "zanje in dawo ,to su momy sukace daganan suka rufo k'ofar khadija ,da fitar malamin gidan duka ya kaure da kururuwa mai firgitarwa daga momy har Jalal sun kasa koda motsi ne ,dama dady bai tashiba tunda yai wanka ,jin girgizar tayi yawa yasa momy shiga bathroom d'inta d'auko buta tana shirin zuba ruwan alwal wasu abubuwa tagani na ban tsoro hakan yasata ficewa tana salati Jalal ne yace "momy to yanxu ya za'ayi ¿ jin momy tayi shiru yasashi kallon inda take kallo ,wata halitta ce mai abin tsoro da girman ta ya zarce tsawon d'akin a sunkuye take tafiya ,idanuwan momy suk k'afe bataji bata gani ,kafin

wanan abin ya iso Jalal cikin tashin hankali ya cici6i momy yai da ita d'aki suna gudu halittar na binsu Allah yabashi ikon rufe k'ofar ba tareda wanan halittar ta shiga ba."

Ruwa yadinga yayafawa momy amma shiru ,a karo na biyu ne ya bud'e ma dai _dai cin fridge d'inta ya ciro ruwan sanyi yana yayyafa mata cikin sa'a ta mik'e tana salati, sallamar malam sukaji babu wanda yai k'ok'arin tashi malamin yace ”yanaga babu kowa Jalal ne cikin d'aga murya yace ” kaje d'akin mara lafiyar ,gamunan momy na ce babu lafiya ,shigewa d'akin malamin yayi daganan yafara adu'oi yana tofa mata yanayi yana tofa mata wata atishawa tayi mai k'arfi wacce tayi dai dai da tashin dady daga bacci ,momy take kira iya k'arfinta ,momy najin muryar Khadija ta fice da sauri tana cewa yaushe rabon da daughter ta kirani, fara'a ce ta baiyyana a fuskarta tashiga d'akin zaune ta sameta ,da shigar momy Khadija tace ” momy maiya faru ne babu komai momy tace ”daganan malamin yace ”hajiya muje parlor inyi miki bayani OK tace suka wuce Khadija tashi tayi ta shiga wanka ,ganin duniyar takeyi kamar sabuwa.*LADIDIN KAUYE*

Page 53 & 54

Malamin ne yace ”dole sai kun kiyaye da shan maganinta to momy tace ”yabasu adu'oi da zasu dingayi a gidan , momy ce tacewa "Khadija ta shirya suje airport itada Khalel , cikin sauri ta nufi d'akinta dan yanzu burinta bai wuce taga mijinta ba , Jalal ne yashigo yana k'walawa khadija kira , fitowa tayi cikin wata shiga mai d'aukar hankali , less ne pink a jikinta sai gyalenta fari takalmi fari jaka pink and wait, wow kuzo kuga Khady , suka shige mota zuwa airport , mutane ne keta saukowa , hango wani had'ad'en saurayi tayi mai kamada Humaid ,tunani tafara kodai humaid ne ?" sanye yake da bak'ar rigar sanyi my adon flawoyi gashi yayi haske sai dai ya rame sosai , da zuwanshi yayi hugging gimbiyarshi , shidai Jalal na gefe yana zaro ido , sunkuceta yayi ya rungumeta yana yimata rad'a a kunne wanda nima banji me suke cewa ba ,Jalal ne yace ”wato ni an manta dani ko ?"dariya Humaid yayi ya doki k'afad'arshi yace ”am sorry kuna raina dukkan ku , mota suka shige ,Humaid da Khadija a Back side ,Jalal yana gaba yana driving,da isarsu gida sukaci karo da anshirya walima gagaruma gurin ya kawatu da flawoyi masu wuta suka shige ciki ."

funny & love story

55_56

Dady da momy suka zauna a kujerun da aka zagaye gurin suna adu'a Jalal ne yace ”bari a yanka cake sai 'intafi gida ,momy ko dariya takeyi farinciki fall zuciyarta ,durk'usawa Humaid yayi ya gaida dady yaje ya gaida momy ya dawo kusada Khadija ya zauna sunci sunsha dan abinci ma daga hotel aka kawo ,misalin k'arfe biyar dady yacewa Humaid ya d'auki matarshi ya wuce ,wanan karon dai Khadija batayi kuka ba, sai da sukayi sallahr isha'i sanan suka d'unguma zuwa gidansu ,hira sukeyi jefi jefi ,da isar su gidan sabon mai gadin da dady 'ya sa musu ya wangale gate d'in yana yimusu sannu da zuwa ,da shigarsu yai parking a ya fito yana mai yiwa Allah godiya ,itama fitowa tayi suka nufi cikin gidan ,kowannensu d'auke da sallama a bakinsu ,da shigarsu parlor suka yada zango Humaid ne ke dariya yana kallon Khadija yace ”baby kingaji ko farr tayi da idonta tace ”yaya mungaji dai cikin sigar tsokana yace ”to gafa tsaraba na kawo miki dan nasan bakya bata kunya tasowa tayi tazo kusa dashi ta zauna wata leda ce mai kyau ya ciro mata gasashiyar kaza ,murna takeyi tana godiya Humaid ne yace ”to yanz mekuma kikeso ,rufe fuska tayi tace ”nakasa tashi d'auko ruwa zansha yana dariya ya mik'e ya d'auko ruwan ,bayan ta cika cikinta ne humaid yace ”to muje muyi alwala yaukam 'zamuyi nafila a sa'a lol."

Hhh wata nafilar aka kumayi akayi adu'oi sosai daganan 'naga Humaid ya sunkuci Khadija yana harara ta ,garin gudu har nakusa fad'uwa 'asbha tagari amarya da 'ango.

Bayan komai ya lafa ne na hango Khadija nata kuka tana cuno baki ,Humaid da fitowarshi daga wanka kenan yace ”haba baby kiyi shiru mana ya marai raice murya kamar mai shirin kuka ,dariyace da kufce mata tace ”kazo ka d'agani 'inka gama tsokanata ,kaya yafara cire mata sanan ya sunkuceta ya kaita bathroom cikin ruwan wankan daya tara mata wani ihu tasa kamar wacce ake shirin cirewa rai can anjima ta lumshe ido sabda zafin ruwan ya ragu ,zubarda wancan yayi yakuma tara wani ,dubanta yayi yace ”to fito inyimiki wanka ,kuka tafara tana yaya dan Allah kaje ka fitomin da kayan dazansa please zanyi da kaina ,zai juya ya hangota ta kwanta kamar wacce ta sami katifa cikin bahon wanka ,dawowa yayi ya fara yimata wankan tana had'ashi da Allah yanayi bai fasa ba."

Nad'ota yayi cikin towel kamar baby hhh ashefa babyn ce ,kwantar da ita yayi a kan gado yafara shafa mata mai , yana gamawa ya d'auko ta ya zaunar da ita gaban dressing mirror ,itadai ta koma kamar photo ko magana batayi powder yafara shafa mata dagan an ya d'auko k'wali ya sanya mata ya d'auko janbaki ya shafa mata hh gurin yin jagira ne yayimata kamar titi fakaceciya dariya sukasa ,gogewa yai yace ”to ainayi mai wuyar ko kinga inda kikayi kyau kuwa hmm kamar sarauniyar kyau , to zomuje kisa kaya ko baby ,kuka zata fara yace ”mai yafaru kuma¿uhm uhm ni yaya bazan iya tafiya ba please help me ,cewa yai uhm uhm nima Ladidi da k'yar nake tafiya ,dariya da kuka ne sukayi nasarar k'wace mata shikuwa yana ganin haka ya sunkuceta ya dirita a gado ,had'ashi ta dingayi da Allah dama ba komai zaiyi mata ba kwai yanason sata yin shiru ne ,cewa yai zonan muyi adu'a ,cikin shagwa6a tace ”yaya kayanfa

?,riga da wando ya ciro mata masu flawoyi a jiki wandon iya gwaiwa ne rigar kuma iya cibiya bayan tasa ne ya kamo hanunta yana sunbatar k'amshin tiraren data fesa yace ”dan Allah ki yafemin Khadija dan Allah ,raahin fahimtar abinda yake cewa yasata kallonshi tace ” yaya ban ganeba ,kukane yayi nasarar kufce masa yace ”nayi miki mumunan zato Khadija asheke cikakiyar budurwa ce nagode da kika kularmin da kanki ,domin duk soyayyar da kuka zuba da buduraka muddin bata tare da budurcin ta to wallahi bazatai daraja a idon mijinta ba ,Khadija ce ta fad'a jikin Humaid tana kuka mai cin rai ,rungumeta yayi yana kwararo mata 'adu'oi akan albarkar rayuwarta ."

Kitchen suka shiga suka had'a breakfast mai rai da lafiya bayan sungama ne Khadija ta zubo musu shikuma Humaid ya shiga wnka ,yana fitowa Khadija ta d'auko wayarshi tafara yimusu photo ,hotuna sukayi kala kala wani ya d'auketa wani kuma tana bayanshi wani kuma ya rungumeta daganan suka zauna cin abinci ,suna gama Humaid yace ”zaije ya dawo insha Allah baze dad'e ba ,rau rau Khadija tayi da ido tana cewa yaya please kaje dane man dariya yasa yace ”to shirya man am sorry sweetheart yanz zandawo afuwan kinji to Allah ya dawo dakai lafiya hubby ,zaro ido yayi yace ”dama inada Suna na musamman shine ake rowar gayamin juyi tayi tace ”yaya kaje ka dawo cikin sauri ya fice sbda Doctor Umar ne yake kiranshi a hospital ."

Misalin k'arfe 1pm Khadija takuma shiga wanka simple makeup tayi ammafa tayi kyau sosai shadda ta d'auko kalar wacce Humaid yasa mai ruwan coffee ba k'aramin kyau shaddar tayi mata ba kasancewar farace sark'a da d'an kunne tasa sai kuma agogon hannu wohuu kamar ka saceta dan kyau, alamar nocking akeyi mai gadi ne ya tambayeta daga ina kike hajiya ? Matar ce tace ”sunanan Rahma to kishiga hajiyanna ciki ,tana isowa part d'in Khadija tafara nocking a nutse Khadija ta fito ganin Anty Rahma ce yasata rungumeta suka shige ciki ,Anty Rahma ce ta kalli Khadija tace ”amarya yakuma k'arin hak'uri alhamdulilh Khadija tace "ta mik'e ta dibowa 'Anty Rahma kayan motsa baki hira sukeyi cikin farinciki tana tabyarta ina yaranta twins dariya anty Rahma tayi tace ”kema ina yimiki fatan hakan rufe fuska Khadija tayi tace ”rainon twins da wahala anty ,sallamar Humaid ce ta katse musu hirarsu wani tsalle Khadija ta doka tatafi da gudu ta dalle bayan Humako.."

Anty Rahma ce tace ”to ni zantafi masoya Khadija na baya ta rufe ido dagan an tacewa anty Rahma bye bye Humaid ne yace ”ina yini ya yara lafiya Lou tace ”daganan tayi gida ,hmm wato khady ko kunya babu 🤭.

Sauketa Humaid yayi yana yimata wani irin kallo afuwan fans gaskiya zaman gidansu Khadija yafi k'arfin mom Islam .

*AFTER TWO MONTHS*

Kwance take kan cinyar Humaid wani amai ne ya taso mata ,kafin yayi yunk'urin mik'ewa ta wankeshi da aman kuka takeyi sosai sbda bak'on yanayin daya ziyarce ta sam batajin dad'in komai a rayuwa ,d'aukarta Humaid yai ya wanke mata jiki ya dawo ya kwantar da ita 'a kan gadonshi ,komawa bathroom yai ya wanka yasakeyi ya shirya ,hijab ya sanya mata ya d'auketa yafice da ita ,bud'e mota yayi yasata 'a back side ya rufe k'ofar ,direct hospital suka nufa da isarsu aka taresu kasancewar halin su kenan kowa na cewa  doctor kak'i dawowa aiki hak'uri yaketa basu kasancewar yanzu hankalinshi ba 'a kwance yake ba ,office d'in doctor Umar ya shiga ganin bai ganshi ba yasashi komawa mota ya rik'o hannun Khadija da ta galabaita ya kaita wani d'aki da babu marasa lafiya ,pitsari yasata yi bayan tayi ne yaje wani lamp ya d'auko abin d'iban jini yana d'iba ya fice test yaje yayi zuwa  minti talatin result ya fito bud'e baki yayi yana kabbara wani doctor Hashim ne yace ” doctor da kanshi yana awo tsabar farinciki Humaid yace ”Hashim yanzu ma zamuje d'akin awon munsami k'aruwa, kowa sai tayashi murna yakeyi."

Khadija dake kwance tanajin kwad'ayin shan tsamiya ta taso tana shirin fitowa sukayi ido biyu da Humaid cewa yai haba baby yazaki wahalarmin da kanki 'ina zaki ,cikin shgwa6a tace ”tsamiya nakeson sha ,zaro ido Humaid yayi yace ”kekuma naki jarabawar kenan¿zata yimai kuka yace ” come down zomuje ayi awo sai mu k'ar6i magani mu wuce kasuwa ,babu musu tabishi suka wuce ana gama mata ya kar6o magani suka shige mota basu sauka a ko ina ba sai kasuwar farar gada ,kayane gasunan na masu ciki irin su tsamiyar biri malmo ali mai ruwa dakuma tsada da agwa luma lol dama wanda na manta haka yadinga jidar mata kayan tsami hhh yaufa babu sha'awar cin kaza saboda wari takeyi mata lol.

Da isarsu gida ya zuzuba mata wasu a fridge  wasu kuma ya wanko mata suka zauna tanata sha ko tayi babu ,hh Humaid da keta k'are mata kallo yace ”Alhamdulilh Allah yabani kyautar mata tagari kuma zata haifamin y'ay'a nagari am very happy wow Khadija bansan da bakinda zankuma yimiki godiya ba please kikula mana  da babyn mu ita dai ko kallonshi batayi ba abinda yafi komai dadi takeshi ammafa a gurinta.

TV Humaid ya kunna NTA wani rahoto ne yaja ra'ayinsu gani nayi Khadija ta tashi ta zauna ,shima Humaid d'in gyara zama yai wani matashin yaro aka nuno hannuwanshi a d'aure yana koro jawabi kamar haka.

_Nidai sunana Ammar d'a  daya tilo ga Alhaji Atiku dollars nataso cikin gata da kulawa a London aka haifeni iyayena basa zama a Nigeria amma ni a Nigeria nake rayuwa ,wani soja dake tsaye ga wasu kuma dake ririke da last speaker suna yimasa tambayoyi to maiya kaika aikatawa y'ar minista fiyad'e ? tsautsayine yace ”a takaice ,wasu tambayoyin aka kuma jeromasa akan cewar kwanaki ankashe mai gadi agidan yaron Alhaji ABDULL... ko zaka iya bamu cikakkiyar amsa eh ninne na kashe shi ,kuma ba shi naso kashewa ba tsohuwar budurwata naso kashewa kokuma mijin da ta aura ,bayan nan ko akwai wani kisan daka ta6ayi babu nasani tawa ta k'are k'arfin arzik'in mahaifina bazai fitar dani daga hannun hukuma ba_.

Daganan aka wuce gurin .

Kukane ya kufcewa Khadija sbda tayi dana sani akan sanin Ammar datayi amma Alhamdulilh tunda gashi a hanun hukuma .

Suna cikin alhinin Ammar sukaji sallama ,Humaid ne ya mik'e jiki a sanyaye bud'e k'ofar yayi yana k'are mata kallo yace Khairat!!!! momy dake baya ta shigo sanye da hijab tace " daughter kinga yarinyar da tayi sanadin ciwonki nan ,mik'ewa Khadija tayi ta fad'a jikin momy ta saki kuka mai tsuma zuciya d'ago kanta tayi tace "momy wanan wacece ?"tsohuwar matar Humaid ce ,momy ce tabata kaff labarin auran Humaid 'dakuma abubuwanda suka faru bayan barinta gida da halin da momy ta shiga ,kuka Khadija takuma sawa ta durk'usa ta rik'e k'afar momy tace "momy dan Allah ki yafemin,dana zauna da baki dinga zubar da hawayenki ba natuba momy ,d'agota momy tayi tace " daughter na yafe miki karki damu kowane bawa da tashi jarabawar ,Khairat ce ta durk'usa 'a gabansu momy tace "dan Allah nima ku yafemin ,nasan na cutar daku gashi ta sanadiyar bin bokaye fuskata ta k'one kowa guduna yakeyi kuma iyayena ma sun tsune min ta had'a hanunwanta biyu tace "dan Allah Ku yafemin kodan guduna da duniya takeyi ,Khadija ce ta d'agota tace "na yafe miki Allah ya yafemana ,Humaid da ko kallonta bayason yi sabda fuskarta tayi abin k'yama yace "indai zaki ficemin a gida to na yafe miki jekiii ya daka mata tsawa momy ma cewa tai ta yafe mata daganan ta fice ,tana fita suka rufo k'ofar d'akin ,jin wani k'ara da wata mota tayi yasasu bud'e get suka fito da gudu ,motace ta kad'e Khairat jini ta baki jini ta hanci ,drivern kuma ya gudu ,cikin azama Humaid yazo ya jijigata jin alamun babu rai a tare da ita yasashi salati momy ma salatin takeyi Khadija kuwa na kuka gidansu ya nufa da ita inda da shigarsu suka tarar da mahaifinta da mahaifiyarta a parlor."

Bayan ya gaishesu ne yake fad'a musu tare da Khairat yazo ,a fusace mahaifin nata ya mik'e yana nuna Humaid yana cewa karta sake ta shigomin gida da k'azamin jikinta mai za'ayi da mazinaciya !!! Kuka Humaid yafara yana cewa dady ku yafe mata motace ta kad'eta kuma babu alamun nunfashi a tare da ita momy a razane tayi waje dady ko ciki ya shige irin ko a jikinshi ,momyn Khairat na ganin ta tafad'i ta suma dady ne ya fito da gudu shima ganin gawar Khairat yasashi nadamar tsa tsauran hukuncin da ya yanke akanta yafa cewa nayafe miki Khairat Allah kayafewa Khairat .

Wayo Allah mutuwa fa ta kori komai a rayuwa kana yawo da gangar jiki baka saniba to y'an uwa mudinga nufar kowa da alkairi mubi umarnin iyayenmu muzamo masu neman za6in Allah.

Gida Khadija suka koma ita da momy sai kuka Allah sarki rayuwa .

********************

Kamar inda kuka sani ne ikon Allah yafi gaban wasa rayuwa tana juyi kala kala wani abin a zahiri wani ko a bad'ini farinciki ko akasin hakan .

AFTER 5 MONTHS

momy na kwance tana bacci aka kirata a waya cewar matar Jalal ta aihu murna bakin momy baya rufuwa ranar suna yaro yaci sunan Baban Khadija wato Musa yaro yasami gata ta kowane 6angare Khadija kuwa tayi rawar gani sosai dan ba'a barta a baya ba ,lokacin cikin Khadija yana 8 months dak'yar take tafiya y'an uwan momy ma sunyi wa yaron shatara ta arzik'i.

Farinciki arzik'i kwanciyar hankali duk familyn sun samu kwanci tashi asarar mai rai cikin Khadija yakai aihuwa zaune take bayanta ya rik'e gakuma mara datasata gaba salati takeyi Humaid dayake kwance yana bacci ya jiyo salatinta ya fito da sauri ganin halin da take cikine yasashi cewa zomutafi hospital ,girgiza kai Khadija tayi tace "insha Allah a gida zan aihu ,nishi takeyi iya k'arfinta Humaid ne yace "kid'an k'ara nishi please kidaure rik'eshi tayi kam kam tasaki wani nishi sai ga yaro ya fad'o tana shirin kwanciya taji wata sabuwar nak'udar Humaid yace "baby gyara na dubaki ,kafin yakai ga dubata sai ga wani yaron yakuma fad'owa ,kuka tafara sosai dan walhi tunda tazo duniya bata ta6a shan zafi kamar haka ba ,Humaid ne ya mutsike yaran da kwa6a6en lalle sbda yana fitarda datti gakuma k'arawa yara lpy bayan mintuna kad'an ya nannad'e yaran ya kwantar dasu kitchen yaje ya juyowa Khadija ruwan zafi ya taimaka mata ya rakata toilet,wanka yayi mata tana cewa da zafi hakadai ya gasa mata jiki ,dawowa yai kan yaran ya tattauna dabino yabasu ya juyo da kunnesu yayi musu kabbara alhamdulih farinciki baiyyane a fuskar Humaid sai da yayiwa yaran wanka ya sanya musu kaya masu kyau sosai dasu safa ,yaga Khadija ta shirya kamar ba mai aihuwa ba sai dai rashin k'arfin jiki ruwan shayi ya had'a mata mai kauri tasha sanan ya kira momy a waya, yake sanar mata ai Khadija ta 'aihu momy ce tace "wanne hospital kokuma kuna nakune ,Humaid ne yace "momy a gida ta 'aihu ,da sauri momy ta d'auko hijab tasa driver ya kaita gidan Khadija ,da isarta gidan d'akin Khadija ta nufa ganin babu kowa yasata komawa parlor ta zauna."

Tace "idan kagama kar6ar aihuwar kafito cikin d'aga murya momy take maganar ,Humaid 'dake kwance ya rungume twins d'inshi ya zaro ido yace "kiyi baccin k'arya please Khady ,rufe idanuwa tayi alamun tana bacci shikuma ya fice parlor gurin momy ,sunkuyar da kai yayi yana sosa keya alakun jin kunya ,momy ce tace "ina daughter tana ciki yace "a tak'aice da shigar momy tasamu Khadija tayi baccin gaske hhh mata anji jiki ☹️ rungume yaran momy tayi tana wani farinciki ,number dady momy ta lalubo ring d'aya ya d'auka ,bayan sun gaisa ne take bashi labarin aihuwar khadija murna fall zuciyar dady barinma dayaji momy tace "yan biyu,

Humaid ne ya shigo bayan ya gaida momy tana cemai ya kar6i aihuwar lafiya ? dariya yasa yace ”momy babu wani abu da 'ake buk'ata eh bbu zaka fitane ,cewar momy Humaid ne yace ”yanzu Doctor Umar yakirani a hospital zanje duba wata bbu lpy OK tom Allah yayi albarka ,amma gobe khadija zata koma gidan mu ba hakan yaso ba 'amma babu inda ya iya yace ”Allah ya kaimu.

Washe gari momy tazo aka shirya kayan Khady dana boys suka nufi gidansu momy ,tana sauka farfesu yayi mata sallama tana zama momy tasa Ummi wato y'ar aikin gidan ta kawo mata citakeyi bakinta babu dad'i bayan tad'anci kad'anne tacewa Ummi tazo ta d'age ,*LADIDIN KAUYE*

funny & love story

57_58

Washe gari Humaid ne yazo cikin wani lallausan yadi blue my kyau fuskar shi sai fitar da tsananin murmishi yakeyi ,kai tsaye d'akin matarshi ya nufa ,sanin yanzu za'a fara yimai katanga da ita ,a hankali ya shige babu wanda ya ganshi ,kwance ya sameta tayi wanka taci kwaliya ,juya idanunsa yai bai saukesu a ko inaba sai akan babys d'insu ,bacci suke sha masha Allah ,ganin baccin ya d'auki Khadija sosai yasashi kwanciya gefenta sunajin nunfashin junya ya rungumeta ,jin d'umin mutum kuma an rungumeta yasa khadija k'ok'arin kwala ihu , Humaid da jikinsa keta rawa ya had'e bakinsu guri d'aya ,wani irin salo yake yimata 'hakan yabata damar k'ara rungumeshi tana lumshe ido ,hmm Khady ayi a hankali dai tamm🤐 Humaid 'da yakejin tsananin buk'atar Khadynshi ya ma manta  jego takeyi yau kwananta uku ,Khadija ce ta dawo cikin hayyacin ta tace ”honey kasan fa momy zata shigo kartazo ta samemu fa ,shii ya sa hannunshi kan lip d'inta don't worry zan 6uya ,zaro ido Khadija tayi tace ”to ka sakeni karta shigo ,matseta yakumayi sbda wani yanayi da yakeji suna cikin hakane momy tafara nocking dan taji k'ofar rufe zaro ido Khadija tayi tana kai dubanta ga Humaid da shima ya zaro nashi kyawawan idanun ,to ya za'ayi ya rad'a mata a kunne ,ka shige toilet kawai kasa key ,mik'ewa yayi ya shige tareda murza key ,momy data gaji da tsayuwa tace ”nikam wane irin bacci kikeyi haka ,Khadija cikin muryar bacci Khadija tace ”momy kiyi hak'uri bacci ne ya d'aukeni ganinan zuwa ,mik'ewa tayi ta gyra wuyan rigarta tare da fuskarta ta shafesu da hannayenta taje bud'ewa momy."

Fad'a momy tafara yimata ya'ayi ta rufe k'ofa bayan tasan ba ita kad'ai bace yanzu in yaran suka tashi suka kuka fa ,shiru tayi tace ”momy kiyi haku'ri bazan sake ba ,shigewa d'akin na

Khadija momy tayi ta fiddo wasu magunguna data tafasa a kettle ta silba cewa tayi tashi da d'uminsa kije ki kama ruwa dashi karfa ki sirka to tace "hhh tunowa tayi ai honey na toilet yasata cewa momy zanyi ,momy cikin bada umarni tace "tashi yanzu ki shiga ina kallonki ,lol babu inda ta iya sbda bata yiwa momy musu ta shige toilet d'in ,ta rufo k'ofa ,lokacin ne momy ta fita ,ganin Humaid tayi yana zaune a gefen bahon wanka dariya tafarayi k'asa k'asa ,Humaid ko haryanzu a tsorace yake amma duk tsoron da yakeji bai hanashi rungumo ta ba cewa tayi to momyn ta tafi please ka koma parlor zanyi tsarki kallon ta yakeyi yana dariya ,to maganin menene aka baki oho tace "a tak'ai ce au bazaki fad'amin ba ?"uhm uhm kwai na masu jego ne ,Khadija tace "lokacinda take shirin tsugunawa ,Humaid da hankalinshi da idanuwanshi duk suna kan Khadija ,lura da hakan yasata cewa mo, aikuwa Humaid ya rufe mata baki ficewa yayi dan yasan zata tona masa asiri kan yaran ya koma yafara yimusu adu'a sanan ya fice .

Yau kwanan Khadija bakwai yaune suna ,d'inkuna kala_kala Humaid yaiwa Khadija sosai sukayi kyau itada yaranta da sukaci sunan Adam da Abdullahi ,kyawawa dasu gashinsu kamar na turawa kuma kyau da dogon hancin duk na Humaid ne sunsha photo inkaga mijin mai jego kamar wanda akayiwa bushara da aljanna ,momy kuwa hidima akeyi sosai babu zama .

Washe gari kowa ya watse sai momy da Khadija a gidan dady yayi tafiya ."

Kwance take tana tunanin halinda mijinta ke shiga lokacinda yaji kewarta d'an halak tafad'a lokacin da taji alamun shigowar mutum Humaid ne sanye da gajeren wando fari ya shigo sad'af² kamar muna fuki key yasawa k'ofar dagan an yakai dubanshi ga Khadija yace "baby gurinki nazo fa tana dariya tace "to bagani ba ,no wai haryanzu shi wanan mai sarautar bai tafiba ,hh ta gane mai yake nufi sarai tace 'to menene hakan measses period uhm yakusa nanda 3 months zaro ido Humaid yayi yace "ko tausayi na bakyani ko yayi alamun kamar yai fushi ,kamoshi tayi ta kwanta saman fafad'an k'irjinshi tana cewa yaya nayi missing ya rufe mata baki da nashi ,am to riders yakamata mu fito daga d'akin mai jego kasancewar lover's sunfara 😀,

Kwance take wani azababen zafi takeji wayo rayuwata ,tafad'a lokacin da Humaid ya mik'ar da ita zai kaita toilet wani rawar jiki yakeyi ,lol ya had'a mata ruwan zafi ta shiga ta jima acikin ruwan maganin butar da momy tabata ,ya zuba ruwan zafi a ciki yace "to yi tsarki da wanan ,bayan ta fito ne ta kar6a tayi tsarki dashi d'aure da towl suka fito rik'e da hannun juna ,Humaid ne ya shafa mai ya zura wandonshi ita ko Khadija bata sauya kayaba sbda tasan momy batada wuyar gano abu ,tana gama tunanin taji sallamar momy ,tunawa tayi yaumafa ta kulle k'ofa ,Humaid dayai nasarar ficewa kafin momy ta shigo ,bud'ewa momy k'ofar tayi ,momy sai kallon fuskar Khadija takeyi kamar mai son gano wani abu ,sunkuyar da kai Khadija tayi tana wasa da fingers d'inta ,murmishi momy tayi tace "humaid ya shigo d'akinan ¿bb a'a.... hhh anan momy ta harbo jirgin zama tayi bakin gadon Khadija tace "wato kunnenki bayajin magana ko daughter ,walhi kika biyewa namiji zakiyi dana sani because shi bashida problem kasancewar su basusan babu ba ko kina nufin gurin da kike tak'ama dashi bazai samu Matsala ba ?to wallahi jego kikeyi kikayi wasa da magungunan danake baki ruwanki ,kuka Khadija tahauyi tana cewa

momy kiyi hak'uri bazan...dakatar da ita momy tayi tace ”inafa bazaki sake ba 'anjima nan zaki sake kemai miji ko hmm gata nake yimiki zomuje ki kar6i farfeshi kici wanan mijin naki 🤐shiru momy tayi lokacin da tabar part d'in Khadija.

Da shigarta bedroom d'in momy kula momy ta mik'o mata wace aka cikata da farfesun kaji yasha yaji da kayan k'amshi bugu da k'ari ga magani kanaci kanajin alamunshi ,zama momy tayi a gefe tana jiran Khadija ta cinye kuma ta shanye romo ,ci Khadija yakeyi dan dauriya ba dan dad'i ba 'ajiye kular tayi tace ”momy na koshi ,spoon momy ta mik'o mata tace ”ungo shanye romon sai anjima ki cinye sauran tafi dashi.

Yauma kamar kullum gogan ya shigo sanye da farar jallabiya Khadija ce ta fad'o masa kawai ya bar hospital ya dawo ganinta samunta yayi tana karanta wani littafi ,salama yai bayan ta 'amsa ne ya d'orata kan cinyarsa ,jin dady wato abdullah na kuka yasa Humaid ciro nono ya d'aukoshi yasa masa a baki ,saida ya k'oshi sanan ya kwantar dashi ,hankalinshi na kan wanan littafin 6oyewa Khadija take k'ok'arin yi amma yafita k'arfi dan haka yayi nasarar k'wacewa ,duba bangon littafin yayi ganin anrubuta *TARAI RAYA* yasa Humaid duban Khadija data rufe fuska janyota yayi yace ”zomu karanta a'a tace ”bacci zanyi, Humaid ne yace ”to zomu kwanta chii daganan labarin ya sauya nafice da gudu 🏃.

Yau kwanan Khadija arba'in dady 'yace gobe zata koma d'akinta momy ma tayarda dan duk wani taku na Humaid kwai kallonsu takeyi amma tasan yawan zuwanshi d'akin KhadijaLADIDIN KAUYE

59_60

Murna sukayi dukkan su biyun amma momy tana tausayawa Khadija ,kiran ta d'aki tayi da zuwanta tace ”Khadija zanja miki kunne akan biyewa Humaid 'da kikeyi kina sakar masa fuska over ,yakamata kigane jego kikeyi karfa 'azo asami matsala ,kinga shi namiji babu ruwansa kezai bari da d'awai niya ,sunkuyar da kai Khadija tayi tana nazarin maganar momy .

Bayan gyara da magunguna datasha daga momy fatarta tayi kyau sosai ga wani shining datakeyi kanan yasha kitso da lalle ga halawa da momy tasa ayi mata kai abindai sai wanda yagani ,washe gari misalin 11:am Humaid ne yai sallama cikin shigar shi ta 'alfarma samun su momy yayi a parlor lokacin suka gama breakfast kasancewar ba da wuri sukeyi ba Khadija na d'akinta tana shirya kayanta tunda momy tace ”sai k'arfe 5:pm zasu tafi.

Durk'usawa yai ya gaida momy ,amsawa tayi cike da kulawa ta mik'e tabar gurin sbda tasan abinda ya kawoshi ,😥ayya mom kin maida Humaid....🤐 kai tsaye d'akin khady ya shige yana yanga yana dariya yau dai gani ga baby na ,ta6e baki Khadija tayi tace "to anfasa ai zaro ido Humaid yayi yace "hhh dana sunkuceki mun wuce ai, dariya suka sa d'aukar yaran yayi yana yimusu adu'a bayan ya gama yace "to tashi muje ,momy data ke shirin shigowa kiran Khadija takawo yaran ayi musu wanka ta tsinto maganar Humaid a sama , yana cewa tashi mutafi ,dubanshi tayi tace " Humaid yaushe kazamo marar kunya ne ?eyye sunkuyar da kansa yayi dan yasan tabbas yayi laifi ,muryar Momy ce tadawo dashi daga hayyacin sa tace "to yanzu ba da bane ka kular min  da yarinya ,insha Allah Humaid yace daganan ya tashi yai gaba ,nasihoyi momy take yiwa Khadija sosai kuma yana shiga kunnen ta."

misalin 5:pm Humaid ya dawo suka wuce shida Khadija ,momy ta sanya musu albarka haka ma dady , fatan alkhairi yayi musu .

Da isar su suka tarar da komai an gyara gidan sai k'amshi yake zubawa ,yada zango Khadija tayi parlor kan d'aya daga cikin kujerun tayada zango ,Dady na hanunta shikuma Humaid Abba ya d'auko ,duka sunyi barci ,d'aukarsu yai d'aya bayan d'aya yaje ya kwantar dasu.

Soyayya suke zubawa sosai Humaid yayi k'iba hakama Khadija sbda momy ta d'aukar mata mai aiki ,watan su Dady da Abba biyu ,Khadija ta tambayi Humaid zuwa k'auye ,baiyi yink'urin hanata ba sbda yasan ta dad'e bata je ba ,sunsa rana kasan cewar gobe weekend ne ,Khadija ce ta kira momy take gaya mata , momy tai farinciki tace "mata subiyo tanan tanada sak'o ."

Washe gari misalin k'arfe goma na safiya ,sun gama shiri kwana biyu Khadija zatayi Humaid kuma 'a ranar zai dawo ,kayanta wanda bata sawa ta loda a d'an ma dai_dai cin akwati suka shige mota ,kai tsaye gidan momy suka nufa ko zama basuyi ba suna gaisawa ta tambayi lpyr yaran ta gansu suka wuce ,tsara sosai Humaid yayiwa su Inna hauwa.

Da isarsu garin Humaid ya kwashe da dariya harda tafawa yace "boys ko inbaku labarin momynku ne yakuma sa dariya ,Khadija ta gano shi sarai ta sha murr taki kulashi sai da suka sukane ya kar6eta yaran ,da sallama suka shiga gidan su inna ,cikin fara'a inna tace "wa'alaikumussalm oyoyo da masu jego ,Sahura dake d'akin inna tana kwaliya tace "to wai suwaye sukazo ne naji kinta wani zumudi ,inna ce tace "y'an binni ne sukazo su Humaidu ,da gudu Khadija ta fito tana washe hak'ora bakinnan yasha jan janbaki ga wani lafcecen Baki a girarta , Khadija ce ta bud'e baki tana cewa Sahura ina zakikai wanan tsayin ,dariya Sahura tayi tace "akwai kayane in kwaso ¿a lokacinne Humaid yai mgna yace "eh suna bayan mota da gudu ta fice tana tsalle Inna ce tace "angirma ba 'asan angirma ba jibeta ,takusa kaiwa waje tajiyo inna tace "ed'in ta murgud'a baki ,kwaso kayan takeyi kamar wata giwa sbda k'arfi da Allah ya zuba mata 'abin ba'a magana.

Ibayan sun shiga d'aki 'inna ta kawo musu fura da nono ,kar6ar yaran tayi ta goya d'aya d'aya kuma yana hannunta ,tsarabar suka mik'awa inna dakuma sak'on momy ,da kayanda Khadija ta kawowa Sahura 'aiko sunyiurna ,mik'ewa Humaid yayi sbda lokacin sallah yayi na azhar

Khadija ma sallar tayi daganan ta kwanta a katifar inna Humaid na dawowa yce zai koma kasancewar yanada ,aiyuka masu yawa .

Washe gari Malam Adamu na yiwa su twins wasa yace "ya Jalal Ipy Lou ai matarsa ta aihu ma ,masha Allah mai aka samu cewar Adamu ,Khadija ce tace "namiji ,sukad'an ta6a yira ,da wuri ta kwanta sbda da wuri zata koma Sahura ko tace "zatabi Khadija babanta yaki yarda wai yayi mata miji karta biyewa samarin binni lol.

Da komawarsu wani zazza6i ya lulu6e Khadija ,Humaid da yashigo yake tambayar yaushe ta dawo ya ganta kwance kamar wacce ta dad'e tana ciwo amai ne yake yunk'urin taso mata ,dagudu tayi toilet tana gamawa ta wanke fuskarta ,
Washe gari hospital suka nufa inda shi da kanshi ya aunata result ne ya fito ganin Khadija na d'auke da cikin wata d'aya yasashi zaro ido ,sbda 'a lokacin Dady da Abba watansu Uku ,magunguna ya had'o musu ita da yaran masu k'ara lafiya ita kuma tana yawan shan fruits farin ciki ya wanzu a wanan familyn sai dai muyi mata adu'ar Allah ya sauketa lpy .

Takuce har kullum mom Islam nayi muku fatan alkairi,abinda nafad'a ba dai_dai ba Allah ka yafemana Allah ka shirya mana zuri'a alhamdulilh🥰🤝.

08141799224👍